

DUNIYA DAYA ADDINI DAYA?

بسم الله الرحمان الرحيم

DUNIYA ƊAYA

ADDINI ƊAYA?

Abubuwan dake ciki

Gabatarwa 4

Kaddarar Allah a kan Talikai domin Shine Mai yawan yin duk abinda Yaso. 5

Asalin ɗan Adam da Addininsa. 15

Farkon kaucewar ɗan Adam daga kan Addini ɗaya 26

Aiko Manzanni don komawa kan Tafarkin Asali na Tauhidi. 34

Aiko Manzon Karshe, Cikamakin Annabawa Shugaban Manzanni Muhammad SAW. 37

Yanayin Al'ummar Duniya a Yau dangane da Addini 44

Koƙarin Kafirai da Mulhidai wajen rusa Addinin Gaskiya a yau 46

Kammalawa. 53

1) GABATARWA

Dukkan Godiya da Yabo su tabbata ga Allah, muna daɗa gode maSa muna neman taimakonSa, muna neman ShiriyarSa da GafararSa kuma muna tuba zuwa gareShi. Haƙiƙa duk wanda Allah Ya shiryar to babu wanda zai iya ɓatar da shi, haka wanda Allah Ya ɓatar babu mai iya shiryar da shi. Ina daɗa shaidawa babu wani da ya cancanci a bauta masa face Allah Shi kaɗai Wanda ba Shi da abokin taraiya, kuma Annabi Muhammadu SAW bawanSa ne kuma ManzonSa ne.

Tsira da Aminci su tabbata ga Annabin Rahama Manzonmu Muhammad ɗan Abdullahi da Sahabbansa da Iyalan gidansa da sauran al'ummar Musulmai dake kan Tafarkin Sunnarsa har Ranar ƙarshe.

Bayan haka,

Al'umma a yau ta kasance a rarrabe dangane da bin Addinai daban-daban. Ko waɗanne Jama'ar wani Addinin, na fatan ragowar Jama'ar wasu Addinan su bar Addininsu su shiga nasu. Misali Musulmai na kwaɗayin kowa ya shiga Musulunci, Kirista na kwaɗayin kowa ya zama Kirista, masu bautar Shanu suna kwaɗayin kowa ya bautawa Saniya, masu bautar Shaiɗan na kwaɗayin kowa ya bautawa Shaiɗan. Marassa Addini suna kwaɗayin kowa ya zama ba shi da Addini. Kowa na watsa farfaganda da Aƙida Sahihiya ko Mummuna domin cimma burinsa.

Shin Duniya za ta iya komawa kan Addini ɗaya ƙwal kamar a can-can baya zamanin Annabi Adamu?

Amsoshin wannan tambaya na cikin Hasken jawabi da Alƙur'ani da Hadithan Manzon Allah SAW suka yi tsokaci, kan rãyuwar ɗan Adam gaba ɗayanta bisa Kaddarar da Allah SWT Ya halicce shi ciki.

Kwanciyar hankalinka, dana kusa da kai, dana nesa da kai, yana cikin fahimtar wannan Al'amari, tare da dogaro ga Allah da bin Shari'arSa cikin Hasken koyarwar Fiyayyen Halitta- Manzon Rahama Muhammad dan Abdullahi (SAW).

2) KADDARAR ALLAH A KAN TALIKAI DOMIN SHINE MAI YAWAN YIN DUK ABINDA YA SO.

Tun farko ya kamata mu san cewar Allah SWT Ya ƙaddara faruwar komai cikin LittafinSa Tsararre watau Lauhul Mahfuz, tun gabanin komai ya kasance (a raye da kuma baiyane cikin bigire da lokaci ƙaiyadadde), a lokacin da Ya ke so da kuma bigiren da Ya ke so. Kuma wannan aiwatar da ƙaddara taShi tana gudana har iya zuwa lokacin da Yake so nan gaba, Zul Jalali wal Ikraam. Duk abinda ba Allah ba, to Taliki ne, watau Allah ne Ya samar da shi, daga babu haka kuma zai karɓi ransa ya koma babu, kuma Bawa ne ga Allah komai girmansa, kuma ko ya so, ko ya ƙi. Manzon Allah a matsayinsa na fiyayyen halitta ga Allah AWJ, bawa ne ga Allah. Kenan shima Allah yake bautawa kuma babu wani mai bauta masa SAW idan ba jahili mushriki ba. Kowa bawa ne na Allah, babu wanda yayi musharaka da shi cikin yin HalittarSa da kula da su da arzurtasu da karɓar ransu da sake dawo musu da shi Ranar Tashi.

2.1 HUJJA DAGA CIKIN ALKUR'ANI

Allah SWT Yana faɗa mana a cikin LittafinSa mai Tsarki:

إن كل من في السماوات و الأرض إلا ءاتي الرحمان عبدا

Dukkan wanda yake a cikin sammai da ƙasa bai zama ba fãce mai jẽ wa Mai rahama ne yanã bãwã. Surah Maryam aya ta 93. Watau idan Kiyama ta tsaya. Kuma haka abin yake yanzu anan duniya.

الله خالق كل شيء و هو على كل شيء وكيل

Allah ne Mai halitta dukan kõme, kuma Shĩ ne Wakĩli a kan kõme. Surah Az-Zumar aya ta 62. Bayan Ya halitta Shine kuma Mai rainonsu da gudanar da al'amarinsu.

و الله خلقكم و ما تعملون

Alhãli, Allah ne Ya halitta ku game da abinda kuke aikatãwa?" Surah Aṣ-Ṣaffat aya ta 96.

فتعالى الله الملك الحق لا إله إلا هو رب العرش الكريم

Allah Mamallakin gaskiya, Yã ɗaukaka. Bãbu abin bautãwa, fãce Shi. Shĩ ne Ubangijin Al'arshi, mai daraja. Surah Al-Muʾminun aya ta 116.

إذ قال ربك للملائكة إني خالق بشرا من طين

فإذا سويته و نفخت فيه من روحي فقعوا له ساجدين

فسجد الملائكة كلهم أجمعون

إلا إبليس استكبر و كان من الكافرين

قال يا إبليس ما منعك أن تسجد لما خلقت بيدي

أستكبرت أم كنت من العالين

قال أنا خير منه خلقتني من نار و خلقته من طين

قال فاخرج منها فإنك رجيم

و إن عليك لعنتي إلى يوم الدين

قال رب فأنظرني إلى يوم يبعثوت

قال فإنك من المنظرين

إلى يوم الوقت المعلوم

قال فبعزتك لأغوينهم أجمعين

إلا عبدك منهم المخلصين

قال فالحق و الحق أقول

لأملأن جهنم منك و ممن تبعك منهم أجمعين

قل ما أسءلكم عليه من اجر و ما أنا من المتكلفين

إن هو إلا ذكر للعالمين

و لتعلمن نبأه بعد حين

A lõkacin da Ubangijinka Ya ce wa malã'iku, "Lalle Nĩ Mai halitta mutum ne daga lãkã.

"Sa'an nan idan Nã daidaita shi, kuma Na hũra (wani abu) daga Ruhĩ Na a cikinsa to ku fãɗi kunã mãsu sujada a gare; shi."

Sai malã'ikun suka yi sujada dukansu, gabã ɗaya.

Fãce Iblis, ya yi girman kai, kuma ya kasance daga kãfirai.

(Allah) Ya ce, "Yã Ibilis! Mẽ ya hana ka, ka yi sujada ga abin da Nã halitta da HannayeNa biyu? Shin, kã yi girman kai ne, kõ kuwa kã kasance daga maɗaukaka ne?"

(Iblis) ya ce, "Nĩ, mafifici ne daga gare shi: Kã halitta ni daga wutã, kuma Kã halitta shi daga lãkã."

(Allah) Ya ce, "To, ka fita daga gare ta, dõmin lalle kai la'ananne ne."

"Kuma lalle a kanka akwai la'anaTa har zuwa rãnar sakamako."

Ya ce (Iblis), "Ya Ubangijina! To, Ka yi mini jinkiri zuwa ga rãnar da ake tãyar da su."

Ya ce (Allah) , "To, lalle kanã daga waɗanda aka yi wa jinkiri,

Zuwa ga yinin lõkaci sananne."

Ya ce (Iblis), "To, inã rantsuwa da buwãyar Ka, lalle, inã ɓatar da su gabã ɗaya.

Fãce bãyin Ka tsarkakakku daga gare su."

(Allah) Ya ce, "To, (wannan magana ita ce) gaskiya. Kuma gaskiya Nake faɗa."

Lalle zã Ni cika Jahannama daga gare ka, kuma daga wanda ya bĩ ka daga gare su, gabã ɗaya"

Ka ce (Ya Muhammad): "Bã ni tambayar ku wani lada a kansa (Alƙur'ani) kuma bã ni daga mãsu ƙãƙalen faɗarsa."

"Shĩ (Alkur'ãn) bai zama ba fãce ambato ne ga dukan halitta."

Kuma lalle zã ku san babban lãbãrinsa a bayan ɗan lõkaci." Suratu Sad aya ta 71 zuwa ta 88

2.1.1 HALITTAR SAMMAI DA AL'ARSHI DA KURSIY.

و هو الذي خلق السماوات و الأرض فى ستة أيام و كان عرشه على الماء ليبلوكم أيكم أحسن عملا و لإن قلت إنكم مبعوثون من بعد الموت ليقولن الذين كفروا إن هاذا إلا سحر مبين

Kuma shi ne wanda Ya halicci sammai da ƙasa a cikin kwanaki shida, kuma Al'arshinSa ya kasance akan ruwa, dõmin Ya jarrabã ku, wanene daga cikinku mafi kyãwon aiki. Kuma haƙĩƙa idan ka ce: "Lalle kũ waɗanda ake tãyarwa ne a bãyan mutuwa," haƙĩƙa waɗanda suka kãfirta sunã cẽwa: "Wannan bai zama ba fãce sihiri bayyananne." Surah Hūd aya ta 7.

بل هو قرءان مجيد

في لوح محفوظ

Ã'aha! Shi Alƙur'ãni ne mai girma.

A cikin Allo tsararre. Surah Al-Burūj aya ta 21, 22.

2.1.2 HALITTAR KASA.

و الأرض وضعها للأنام

فيها فاكهة و النخل ذات الأكمام

و الحب ذو العصف و الريحان

فبأى ءالآء ربكما تكذبان

"Kuma ƙasã Yã aza ta dõmin tãlikai."

"A cikinta akwai 'ya'yan itãcen marmari da dabĩno mai kwasfa."

"Da ƙwãya mai sõshiya da ƙamshi."

"To, sabõda wanne daga ni'imõmin Ubangjinku kuke ƙaryatãwa?" Surah Ar-Raḥman aya ta 10 - 13

الله الذي رفع السماوات بغير عمد ترونها ثم استوى على العرش و سخر الشمس و القمر كل يجرى لأجل مسمى يدبر الأمر يفصل الآيات لعلكم بلقاء ربكم توقنون

و هو الذى مد الأرض و جعل فيها رواسي و أنهارا و من كل الثمرات جعل فيها زوجين اثنين يغشى اليل النهار إن فى ذلك لآيات لقوم يتفكرون

و فى الأرض قطع متجاورات و جنات من أعناب و زرع و نخيل صنوان و غير صنوان يسقى بماء واحد و يفضل بعضها على بعض فى الأكل إن فى ذلك لآيات لقوم يعقلون

Allah Shi ne wanda Ya ɗaukaka sammai, bã da ginshiƙai ba waɗanda kuke ganin su. Sa'an nan kuma Ya daidaita a kan Al'arshi, kuma Ya hõre rãnã da watã, kõwane yanã gudãna zuwa ga ajali ambatacce. Yanã shirya al'amari, Yanã rarrabe ãyõyi daki-daki, mai yiwuwa ne ku yi yaƙĩni da haɗuwa da Ubangijinku.

Kuma shĩ, ne wanda Ya shimfiɗa kasa, kuma Ya sanya duwãtsu da kõguna a cikinta, kuma daga dukan 'ya'yan itãce Ya sanya ma'aura biyu cikinsu. Yanã sanya dare ya rufe yini. Lalle ne a cikin wancan, haƙĩƙa akwai ãyõyi ga mutãne waɗanda suke yin tunãni.

Kuma a cikin ƙasa akwai yankuna mãsu maƙwabtaka, da gõnaki na inabõbi da shũka da dabĩnai iri guda, da waɗanda bã iri guda ba, anã

shayar da su da ruwa guda. Kuma Munã fĩfĩta sãshen sa a kan sãshe a wajen ci. Lalle ne a cikin wancan akwai ãyõyi ga muiãne waɗan da suke hankalta. Surah Ar-Raʿd aya ta 2-4.

و ما من دابة فى الأرض إلا على الله رزقها و يعلم مستقرها و مستودعها كل فى كتاب مبين

Kuma bãbu wata dabba a cikin ƙasa fãce ga Allah arzikinta yake, kuma Yanã sanin matabbatarta da ma'azarta, duka sunã cikin littãfi bayyananne. Surah Hūd aya ta 6.

الله الذى خلق السماوات و الأرض و ما بينهما فى ستة أيام ثم استوى على العرش ما لكم من دونه من ولي و لا شفيع أفلا تتذكرون

يدبر الأمر من السماء إلى الأرض ثم يعرج إليه فى يوم كان مقداره ألف سنة مما تعدون

ذلك عالم الغيب و الشهادة العزيز الرحيم

Allah ne wanda Ya halitta sammai da ƙassai da abin da yake a tsakãninsu a cikin kwãnuka shida, sa'an nan Ya daidaita a kan Al'arshi. Bã ku da, baicin Shi, wani majiɓinci kuma babu wani maceci. Shin, bã zã ku yi tunãni ba?

Yanã shirya al'amari daga sama zuwa ga ƙasã, sa'an nan ya tãka zuwa gare Shi a cikin yini, wanda gwargwadonsa shẽkaru dubu ne ga abin da kuke lissafãwa.

Wannan shĩ ne Masanin fake da bayyane, Mabuwãyi, Mai jinƙai. Surah As-Sajdah aya ta 4 zuwa ta 6.

2.1.3 KADDARAR ALLAH SWT A KAN ƊAN ADAM DA ALJAN

و لقد ذرأنا لجهنم كثيرا من الجن و الإنس لهم قلوب لا يفقهون بها و لهم أعين لا يبصرون بها و لهم ءاذان لا يسمعون بها أولاءك كالأنعام بل هم أضل أولاءك هم الغافلون

Kuma lalle ne, haƙĩƙa, Mun halitta sabõda Jahannama, mãsu yawa daga aljannu da mutãne, sunã da zukãta, ba su fahimta da su, kuma sunã da idãnu, bã su gani da su, kuma sunã da kunnuwa, ba su ji da su; waɗancan kamar dabbobin gida suke. Ã'a, sũ ne mafi ɓacẽwa; Waɗancan sũ ne gafalallu." Surah Al-Aʿraf aya ta 179.

و لو شءنا لآتينا كل نفس هداها و لاكن حق القول مني لأملأن جهنم من الجنة و الناس أجمعين

Kuma dã Mun so dã Mun bai wa kõwane rai shiriyarsa, to amma magana ta tabbata daga gare Ni! Lalle ne Inã cika Jahannama daga aljannu da mutãne gabã ɗaya. Surah As-Sajdah aya ta 13.

يسبح لله ما فى السماوات و ما فى الأرض له الملك و له الحمد و هو على كل شيء قدير

هو الذي خلقكم فمنكم كافر و منكم مؤمن و الله بما تعملون بصير

"Abinda yake a cikin sammai da wanda yake a cikin ƙasã sunã tasbĩhi ga Allah. Gare Shi mulki yake, kuma gare Shi gõdiya take. Kuma Shi, a kan kõme, Mai ikon yi ne."

"Shĩ ne wanda Ya halitta ku. Sa'an nan daga gare ku akwai kãfiri kuma daga gare ku akwai mũmini. Kuma Allah Mai gani ne ga abinda kuke aikatãwa." Surah At-Taghabun aya ta 1-2.

Waɗannan ayoyi suna tsokaci kan cewa lallai kowanne lokaci a doron ƙasar nan, sai an sami masu biyayya ga Addinin Allah da Kuma kangararru maƙiya Addinin Allah. Saboda haka, me yasa zaka damu kanka har ka sami ƙuncin zuciya akan kafurai da mushrikai da 'yan bidi'a, da yan duba, bokaye da yan tsibbu da sauran matsafa?

Idan Allah Ya ƙaddara maka kasancewa cikin na gari masu bin Allah cikin Addinin da Allah Ya Shar'anta a bi a lokacinka ba tare da ka yi

shirka da Allah ba, sai kayi ta godewa Allah tare da Addu'ar dauwama akai, ba tare da ka zame ba har mutuwarka. Domin zaɓi ne daga Allah SWT a kanka, ba dabarar ka ce ko ƙarfin ka ba.

Ragowar kuma waɗanda ba irinka ba, tausaya musu za kayi tare da yi musu Addu'ar SHIRIYA. Ba gaba da ƙiyayya za kayi dasu ba ta fitar hankali wadda ta sãɓãwa Shariya. Ba kuma amincewa za kayi da su ba cikin duk son zuciyar da suka zo da shi wanda ya sãɓãwa abinda kake kai. "No compromise abinda Bature yake cewa" cikin Addinin ka.

2.2 HUJJA DAGA AHADITH

Imam Ahmad, At-Tirmidhi V4 H2155, Abu Dawud, Hadithin Alƙalami (Pen).

حدثنا يحيى بن موسى قال حدثنا أبو داودالطيالسي قال حدثنا عبد الواحد بن سليم قال قدمت مكة فلقيت عطاء بن ألي رباح فقلت له يا أبا محمد إن أهل البصرة يقولون في القدر قال يا بني أتقرأ القرءآن ؟ قلت نعم قال فاقرأ الزخرف قال فقرأت : حم والكتاب المبين إنا جعلناه قرآنا عربيا لعلكم تعقلون و إنه في أم الكتاب لدينا لعلي حكيم [الزخرف] فقال أتدري ما أم الكتاب ؟ قلت الله و رسوله أعلم قال فإنه كتاب كتبه الله قبل أن يخلق السموات و قبل أن يخلق الأرض فيه إن فرعون من أهل النار و فيه تبت يدا أبي لهب و تب قال عطاء : فلقيت الوليد بن عبادة بن الصامة صاحب رسول الله صلى الله عليه و سلم فسألته ما كانت وصية أبيك عند الموت ؟ قال : دعاني أبي فقال لي : يا بني اتق الله و اعلم أنك لن تتقي الله حتى تؤمن بالله و تؤمن بالقدر كله خيره و شره فإن من على غير هذا دخلت النار إني سمعت رسول الله صلى الله عليه و سلم يقول : إن أول ما خلق الله القلم فقال : أكتب : فقال ما أكتب ؟ قال : أكتب القدر ما كان و ما هو كاءن إلى الأبد : و هذا حديث غريب من هذا الوجه

2155. 'Abdul-Waahid bin Sulaim ya faɗi cewar "Na iso Makkah sai na hadu da 'Ada'a bin Abi Rabaha. Sai nace masa "Ya Abu Muhammad, mutanen Al-Barah suna magana akan Kaddara". Sai ya ce "Ya ɗana, ai kana karanta Alƙur'ani ko?" Na ce masa E, sai ya ce "to karanta mini Az-

Zukhruf." Sai na karanto masa: "Ha Mim". "Ina rantsuwa da Littãfi Mabayyani". "Lalle Mũ, Mun sanya shi abin karãtu na Lãrabci, tsammãninku, kunã hankalta." "Kuma lalle, shĩ, a cikin Uwar Littãfi a wurin Mu, haƙĩƙa, Maɗaukaki ne, Bayyananne." Sai yace kasan mecece Uwar Littafi? Sai na ce Allah da ManzonSa ne suka fi sani. Sai yace "Wani Littafi ne (Lauhul Mahfouz) da Allah Ya rubuto kafin halittar Sammai da ƙasa. A cikinsa an rubuta "Fir'auna yana cikin 'yan Wuta." A cikinsa an rubuta "Hannaye biyun Abu Lahab sun tabe, Shima kuma ya tabe." Ada'a yace na gamu da Al-Ḥadid ɗan Ubadah bin As-Samit sahabin Manzon Allah SAW sai na tambayeshi "mecece wasiyyar da Mahaifinka yayi maka kafin ya bar duniya?" Sai ya ce ya Kira ni ya ce mini "Ya ɗana ka ji tsoron Allah kuma ka sani baza ka taɓa Jin tsoron Allah ba har sai kayi Imani da Shi kuma ka yi Imani da Kaddara mai kyau da maras kyau. Idan ka mutu ba akan wannan ba, za ka shiga Wuta ne. Haƙiƙa Na ji Manzon Allah SAW yace "Tabbas abinda Allah Ya fara halitta shine Alƙalami. Sai Ya cewa Alƙalami "Rubuta". Alƙalami ya ce me zan rubuta? Sai Ya ce "Rubuta KADDARA abinda ya kasance da abinda zai kasance har abada". Hadithi ne Sahihi. At-Tirmidhi.

حدثنا قتيبة بن سعيد حدثنا مغيرة بن عبد الرحمان القريسي عن أبي الزياد عن الأرج عن أبي هريرة رضي الله عنه قال قال رسول الله صلى الله عليه و سلم "لما قضى الله الخلق كتب في كتابه فهو عنده فوق العرش "إن رحمتي علبت غضبي

3194. Abu Hurairata yace: na ji Manzon Allah SAW ya ce "Lokacin da Allah Ya hukunta yin Halitta Ya rubuta a cikin LittafinSa wanda yake tare da Shi a kan Al-Arshi "RahamaTa ta rinjayi fushiNa". Bukhari 3194, ko 3201 a wannin bugun na Bukhari. Duba (Nasa'i Al-Kubra 4/417 - 7750).

(Tafsir At-Dabari)

Ibn Jarrer At-Ɗabari ya ce: Yunus ya faɗa mini, shi kuma Ibn Wahb ya ce: Ibn Zaid ya faɗa: babana ya faɗa mini cewar Manzon Allah SAW ya ce: Game da girman Kursi, duniya da farfajiyar sararin Subuhana ba su fi girman Dirhami bakwai da aka watsa akan garkuwa ba. Abu Zarr ya ce: Na ji Manzon Allah SAW yana cewa: kwatankwacin girman Kursi akan Al-Arshi bai kai girman zoben da aka jefa cikin sahara a doron ƙasa ba. (Watau Kursi ta ɓata ɓat a cikin Al-Arshi, to ina kuma ga Girman Allah?). Wannan Hadithi ingantacce ne daga At-Ɗabri.

3) ASALIN ƊAN ADAM DA ADDININSA.

Ɗan Adam halittace da Allah SWT Ya halitta da HannayenSa biyu tun Asali.

Maganar Darwin ko aƙidar Darwism ƙarya ce ƙerarriya, marras asali cikin dukkan Addinan da aka saukar daga sama. Ba wai wata halittace ta daban a cikin ruwa ba, wadda ta rikiɗe ta zama ɗan Adam ta dawo kan tudu ta bar cikin teku. Halittun ruwa da ban suke da na kan tudu. Na kan tudunma sun rarrabu, akwai masu tafiya kan ƙafofi biyu, wasu kan ƙafofi huɗu, wasu masu jan ciki, wasu masu tashi sama. Kowanne an hore masa inda zai rayu har zuwa mutuwarsa abar ƙaiyadewa.

Tun Asali haka Allah Ya halicce shi kuma yake nan haka har yanzu. Kamar yadda saniya, tattabara, sauro, ƙadangare, da bishiyar ayaba, lemo, inibi, suke tun Asalin halittarsu ta farko, to har yau ɗinnan haka suke. Canjin kawai shine na girman giki. Abinda yake ya sami abinci da lafiya, yayi jibgege ƙato da kyan jikin, abinda bai sami abinci lafiyayye ba, ga kuma cuta ya motse. Amma dai shine tun asalinsa. Shi ya sanya, Allah cikin HikimarSa Ya ƙaddara aure, jima'i, ɗaukar ciki, haihuwa da raino, domin kiyaye halittar Asalin. Kuma haka abin yake ga tsirrai da

ragowar dabbobi na ruwa da kan tudu. Yana ɗaya daga cikin dalilai domin kiyaye halittar Asali, doka cikin Addinin Musulunci cewar duk wanda ya yi jima'i da dabba, a kashe dabbar tare da shi. Haka dan luwaɗi da 'yar maɗugo duk a yi musu mummunan kisa, da wanda yake yi da wanda ake yiwa. Canza Halitta mummunan zunubi ne a Addinin Musulunci. Allah Ne Mafi sani.

3.1 HUJJA DAGA ALKUR'ANI.

3.1.1 SAMUWAR ƊAN ADAM.

و إذ قال ربك للملائكة إني جاعل في الأرض خليفة قالوا أتجعل فيها من يفسد فيها و يسفك الدماء و نحن نسبح بحمدك و نقدس لك قال إني أعلم ما لا تعلمون

Kuma a lõkacin da Ubangijinka Ya ce ga malã'iku: "Lalle ne, Ni Mai sanya wani halĩfa ne a cikin ƙasa," suka ce: "Ashe, zã Ka sanya a cikinta, wanda zai yi ɓarna a cikinta, kuma mu, muna yi maka tasbihi tare da gõde maka, kuma muna tsarkakewa gareka" Ya ce: "Lalle ne, Ni Na san abin da ba ku sani ba." Surah Al-Baqarah aya ta 30.

إذ قال ربك للملائكة إني خالق بشرا من طين

A lõkacin da Ubangijinka Ya ce wa malã'iku, "Lalle Nĩ Mai halitta mutum ne daga lãkã. Surah Ṣād aya ta 71.

الذي أحسن كل شيء خلقه و بدأ خلق الإنسان من طين

ثم جعل نسله من سلالة من ماء مهين

ثم سواه و نفخ فيه من روحه و جعل لكم السمع و الأبصار و الأفـءدة قليلا ما تشكرون

و قالوا أءذا ضللنا في الأرض أءنا لفي خلق جديد بل هم بلقاء ربهم كافرون

قل يتوفاكم ملك الموت الذي وكل بكم ثم إلى ربكم ترجعون

Wanda Ya kyautata kõme, Wanda Ya halitta shi. Shi ne kuma Ya fãra halittar mutum daga lãka.

Sa'an nan Ya sanya ɗiyansa daga wani asali na wani ruwa wulãkantacce.

Sa'an nan Ya daidaita shi, kuma Ya hũra a cikinsa, daga ruhinSa kuma Ya sanya muku ji, da ganunuwa da zukãta. Gõdiyarku kaɗan ce ƙwarai.

Kuma suka ce: "Shin, idan mun ɓace a cikin ƙasã, shin, lalle mu, tabbas ne munã zama a cikin wata halitta sãbuwa?" Ã'a, su game da gamuwa da Ubangijinsu kãfirai

Ka ce: "Mala'ikan mutuwa ne. wanda aka wakkala a gare ku, shĩ ne ke karɓar rãyukanku.* Sa'an nan zuwa ga Ubangijinku ake mayar da ku." Surah As-Sajdah aya ta 7 zuwa ta 11.

و لقد خلقنا الإنسان من سلالة من طين

ثم جعلناه نطفة في قرار مكين

ثم خلقنا النطفة علقة فخلقنا العلقة مضغة فخلقنا المضغة عظاما فكسونا العظام لحما ثم أنشأناه خاقا ءاخر فتبارك الله أحسن الخالقين

ثم إنكم بعد ذالك لميتون

ثم إنكم يوم القيامة لتبعثون

Kuma lalle ne, haƙĩka, Mun halitta mutum daga wani tsantsa daga lãka.

Sa'an nan kuma Muka sanya shi, ɗigon maniyyi a cikin matabbata natsattsiya.

Sa'an nan kuma Muka halitta shi gudan jini, sa'an nan Muka halitta gudan jinin tsõka, sa'an nan Muka halitta tsõkar ta zama ƙasũsuwa,

sa'an nan Muka tufãtar da ƙasũsuwan da wani nãma sa'an nan kuma Muka ƙãga shi wata halitta dabam. Sabõda haka albarkun Allah sun bayyana, Shi ne Mafi kyawun mãsu halittawa.

Sa'an nan kuma ku, bãyan wannan, lalle ne masu mutuwa ne.

Sa'an nan kuma lalle ne kũ a Rãnar alkiyãma, za a tãyar da ku," Surah Al-Muʾminūn aya ta 12 zuwa ta 16.

سبحان الذي خلق الأزواج كلها مما تنبت الأرض و من أنفسهم و مما لا يعلمون

Tsarki ya tabbata ga Wanda Ya halitta nau'uka, namiji da mace, dukansu, daga abin da ƙasã ke tsirarwa, kuma daga kansu, kuma daga abin da basu sani ba. Surah Ya-Sin aya ta 36.

3.1.2 KARRAMA ƊAN ADAM, SAUKO DA SHI DUNIYA DA KARƁAR TUBARSA.

و إذ قلنا للملائكة اسجدوا لآدم فسجدوا إلا إبليس أبى و استكبر و كان من الكافرين

و قلنا يآ ءادم اسكن أنت و زوجك الجنة و كلا منها رغدا حيث شءتما و لا تقربا هذه الشجرة فتكونا من الظالمين

فأزلهما الشيطان عنها فأخرجهما مما كانا فيه و قلنا اهبطوا بعضكم لبعض عدو و لكم في الأرض مستقر و متاع إلى حين

فتلقى ءادم من ربه كلمات فتاب عليه إنه هو التواب الرحيم

قلنا اهبطوا منها جميعا فإما يأتينكم مني هدى فمن تبع هداى فلا خوف عليهم و لا هم يحزنون

Kuma a lõkacin da Muka ce ga malã'iku: "Ku yi sujada ga Ãdam," Sai suka yi sujada, fãce Ibilĩsa ya ƙi, kuma ya yi girman kai, kuma ya kasance daga kãfirai.

Kuma muka ce: "Ya Ãdam! Ka zauna kai da matarka a gidan Aljanna, kuma ku ci daga gare ta, bisa wadãta, inda kuke so, kuma kada ku kusanci wannan itãciyar, har ku kasance daga azzãlumai."

Sai Shaiɗan ya talãlãɓantar da su ga barinta, sai ya fitar da su daga abinda suka kasance a cikinsa. Kuma Muka ce: "Sãshenku nã maƙiyi ga sãshe, kuma kuna da a cikin ƙasa matabbata da jin dãɗi zuwa ga wani lõkaci."

Sai Ãdam ya karɓi wasu kalmõmi daga Ubangjjinsa, sabõda haka Ya karɓi tũba a kansa. Lalle ne Shi, Shĩ ne Mai karɓar tũba, Mai jin ƙai.

Muka ce: "Ku ku sauka daga gare ta gabã ɗaya. To, imma lalle shiriya ta je muku daga gare Ni, to, wanda ya bi shiriya ta to, bãbu tsõro a kansu, kuma bã su yin baƙin ciki." Surah Al-Baqarah aya ta 34 zuwa 38.

و لقد كرمنا بني ءادم و حملناهم في البر و البحر و رزقناهم من الطيبات و فضلناهم على كثير ممن خلقنا تفضتلا

Kuma lalle ne Mun girmama 'yan Adam, kuma Muka ɗauke su a cikin ƙasa da tẽku kuma Muka azurta su daga abũbuwa mãsu dãɗi kuma Muka fĩfĩta su a kan mãsu yawa daga waɗanda Muka halitta, fĩfĩtãwa." Surah Al-Isra'i aya ta 70.

3.1.3 AIKO DA SHIRIYA (ADDINI) GA ƊAN ADAM DA ALJAN.

شرع لكم من الدين ما وصى به نوحا و الذي أوحينا إليك و ما وصينا به إبراهيم و موسى و عيسى أن أقيموا الدين و لا تتفرقوا فيه كبر على المشركين ما تدعوهم إليه الله يجتبى إليه من يشاء و يهدى إليه من ينيب

"Ya shar'anta muku, game da addini, abinda Ya yi wasiyya da shi ga Nũhu (Noah) da abinda Muka yi wahayi da shi zuwa gare ka (Ya Muhammad), da abinda Muka yi wasiyya da shi ga Ibrãhĩm (Abraham) da Mũsã (Moses) da Ĩsã (Jesus), cẽwa ku tsayar da addini sõsai kuma kada ku rarrabu a cikinsa. Abinda kuke kira zuwa gare shi (cewa a bautawa Allah ɗaya Tilo) ya yi nauyi a kan mãsu shirki. Allah na zãɓen wanda Yake so zuwa gare Shi, kuma Yanã shiryar da wanda ke tawakkali gare Shi, ga hanyarSa." Suratu Ash-Shura aya ta 13.

الم

تنزيل الكتاب لا ريب فيه من رب العالمين

أم يقولون افتراه بل هو الحق من ربك لتنذر قوما ما اتاهم من نذير من قبلك لعلهم يهتدون

Alif, Lām, Meem.

Saukar da Littafin bãbu shakka a gare shi, daga Ubangijin tãlikai yake.

Kõ sunã cẽwa (Muhammadu ne) ya ƙirƙira shi? Ã'a, shĩ ne gaskiya daga Ubangijinka, dõmin ka yi gargaɗi ga mutãne waɗanda wani mai gargaɗi bai je musu ba a gabãninka, fãtan zã su shiryu. Surah As-Sajdah ta 1 zuwa ta 3.

و ما أرسلنا من قبلك من رسول إلا نوحي إليه أنه لا إله إلا أنا فأعبدون

Kuma ba Mu aiki wani Manzo ba a gabãninka fãce Munã yin wahayi zuwa gare shi, cẽwa "Lalle ne Shi, bãbu abin bautãwa fãce Ni (Allah), sai ku bauta Mini." Surah Al-Anbiya aya ta 25.

و لقد أنزلنا إليكم ءايات مبينات و مثلا من الذين خلوا من قبلكم و موعظة للمتقين

Kuma lalle ne Mun saukar zuwa gare ku, ãyõyi mãsu bayyanãwa, da misãli daga waɗanda suka shige daga gabãninku, da wa'azi ga mãsu taƙawa. Surah An-Nur aya ta 34.

الذين ءامنوا و لم يلبسوا إيمانهم بظلم أولاءك لهم الأمن و هم مهتدون

"Waɗanda suka yi ĩmãni, kuma ba su gauraya ĩmãninsu da zãlunci ba, waɗannan sunã da aminci, kuma sũ ne shiryayyu." Surah Al-Anʿām aya ta 82.

و وصى بها إبراهيم بنيه و يعقوب يا بني إن الله اصطفى لكم الدين فلا تموتن إلا و أنتم مسلمون

أم كنتم شهداء إذ حضر يعقوب الموت إذ قال لبنيه ما تعبدون من بعدي قالوا نعبد إلاهك و إله ءاباءك إبراهيم و إسماعيل و إسحاق إلها واحدا و نحن له مسلمون

تلك أمة قد خلت لها ما كسبت و لكم ما كسبتم و لا تسألون عما كانوا يعملون

"Kuma lbrãhĩm(Abraham) ya yi wasiyya da ita ga ɗiyansa, kuma Ya'aƙũbu (Jacob) (ya yi wasiyya, suka ce:) "Yã ɗiyãna! Lalle ne, Allah Ya zãɓã muku addini don haka kada ku mutu, lalle, fãce kuna Musulmi."

"Ko kun kasance halarce a lõkacin da mutuwa ta halarci Ya'aƙũbu (Jacob), a lõkacin da ya ce wa ɗiyansa: "Mẽne ne zã ku bautawa daga bãyãna (idan na rasu)?" Suka ce: "Muna bautawa Abin bautawarka kuma Abin bautawar ubanninka lbrãhĩm (Abraham) da lsmã'ĩla (Ishmael) da Is'hãƙa (Isaac), Ubangiji Guda, kuma mu a gare Shi mãsu miƙa wuya ne."

"Waccan, wata al'umma ce, ta riga ta shige, tana da abin da ta sanã'anta kuma kuna da abin da kuka sanã'anta, Kuma bã zã a tambaye ku ba daga abinda suka kasance suna aikatãwa." Surah Al-Baqarah aya ta 132 zuwa ta 134.

3.1.4 JAN HANKALIN ƊAN ADAM A KAN YA GUJI SHAIƊAN DA RUNDUNARSA SANNAN KADA YA YADDA YA MUTU YANA KAFIRI, (SHINE DUK WANDA BAI YARDA DA MUSULUNCIN DA ANNABI MUHAMMAD SAW YA ZO DA SHI BA).

يا أيها الناس إن وعد الله حق فلا تغرنكم الحياة الدنيا و لا يغرنكم بالله الغرور

إن الشيطان لكم عدو فاتخذوه عدوا إنما يدعوا حزبه ليكونوا من أصحاب السعير

الذين كفروا لهم عذاب شديد و الذين ءامنوا و عملوا الصالحات لهم مغفرة و أجر كبير

أفمن زين له سوء عمله فرءاه حسنا فإن الله يضل من يشاء و يهدي من يشاء فلا تذهب نفسك عليهم حسرات إن الله عليم بما يصنعون

Yã kũ mutãne! Lalle wa'adin Allah gaskiya ne, sabõda haka kada rãyuwar dũniya ta rũɗar da ku, kuma kada marũɗi ya rũɗe ku game da Allah.

Lalle Shaiɗan (Satan) maƙiyi ne a gare ku, sai ku riƙe shi maƙiyi. Yanã kiran ƙungiyarsa kawai ne, dõmin su kasance 'yan Wutar sa'ir.

Waɗanda suka kãfirta suna da azãba mai tsanani kuma waɗanda suka yi ĩmãni kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, sunã da wata gãfara da sakamako mai girma.

Shin to, wanda aka ƙawãta masa aikinsa, har ya gan shi mai kyau (yanã daidai da waninsa)? Sabõda haka, lalle, Allah Yanã ɓatar da wanda Yake so, kuma Yanã shiryar da wanda Yake so, sabõda haka kada ranka ya halaka a kansu dômin baƙin ciki. Lalle Allah Masani ne ga abinda suke sanã'antawa. Surah Faɗir aya ta 5 zuwa ta 8.

إن الذين كفروا و ماتوا و هم كفار ألاءك عليهم لعنة الله و الملائكة و الناس أجمعين

خالدين فيها لا يخفف عنهم العذاب و لا هم ينظرون

و إلاهكم إله واحد لا إله إلا هو الرحمان الرحيم

"Lalle ne, waɗanda suka kãfirta kuma suka mutu alhãli kuwa suna kãfirai, waɗannan akwai, a kansu, la'anar Allah da Malã'iku da mutãne gabã ɗaya."

"Suna madawwama a cikin ta, bã a sauƙaƙa Azãba daga barinsu, kuma ba su zama ana jinkirta musu ba."

"Kuma Ubangijinku Ubangiji Guda ne. Bãbu wani Ubangiji fãce Shi, Mai rahama, Mai jin ƙai." Surah Al-Baqarah aya ta 161 zuwa ta 163.

يآ أيها الذين ءامنوا ادخلوا في السلم كآفة و لا تتبعوا خطوات الشيطان إنه لكم عدو مبين

فإن زللتم من بعد ما جاءتكم البينات فاعلموا أن الله عزيز حكيم

"Yã ku waɗanda suka yi ĩmani! Ku shiga cikin Musulunci gabã ɗaya; kuma kada ku bi zambiyõyin Shaiɗan; lalle ne shĩ a gare ku maƙiyine, bayyanan ne."

"To, idan kun karkace daga bayan hujjõji bayyanannu sun zo muku to ku sani cẽwa lalle ne Allah, Mabuwãyi ne, Mai hikima." Surah Al-Baqarah aya ta 208 da 209.

إن الذين كفروا لن تغني عنهم أموالهم و لا أولادهم من الله شيئا و أولاءك وقود النار

كدأب ءال فرعون و الذين من قبلهم كذبوا بآياتنا فأخذهم الله بذنوبهم و الله شديد العقاب

"Lalle ne waɗanda suka kãfirta, dũkiyõyinsu bã su tunkuɗe musu kõme daga Allah, kuma 'ya'yansu bã su tunkuɗẽwa, kuma waɗannan, sũ ne makãmashin wuta."

"Kamar ɗabi'ar mutãnen Fir'auna da waɗanda ke a gabãninsu, sun ƙaryata ãyõyinMu, sai Allah Ya kãmã su sabõda zunubansu, kuma Allah Mai tsananin uƙũba ne." Surah Ali-ʿImran aya ta 10 da 11

إن الذين كفروا و ماتوا و هم كفار فلن يقبل من أحدهم ملء الأرض ذهبا ولو افتدى به أولاءك لهم عذاب أليم وما لهم من ناصرين

"Lalle ne wanɗanda suka kãfirta, kuma suka mutu alhãli kuwa suna kãfirai to bã zã a karɓi cike da ƙasa na zinãri daga ɗayansu ba, kõ dã ya yi fansa da shi, waɗannan sunã da azãba mai raɗaɗi, kuma bã su da wasu mataimaka." Surah Ali-ʿImran aya ta 91.

3.2 HUJJA DAGA AHADITH.

3.2.1 SAMUWAR ƊAN ADAM ('YAN ALJANNA DA 'YAN WUTA)

حدثنا عبد بن حميد قال حدثنا أبو نعيم قال حدثنا هشام بن سعد عن زيد بن أسلم عن أبي صالح عن أبي هريرة قال قال رسول الله صلى الله عليه و سلم : لما خلق الله آدم مسح ظهره فسقط من ظهره كل نسمة هو خالقها من ذريته إلى يوم القيامة و جعل بين عيني كل إنسان منهم وبيصا من نور ثم عرضهم على آدم فقال أي رب من هاؤلاء ؟ قال هاؤلاء ذريتك فرأى رجلا منهم فأعجبه وبيص مابين عينيه فقال أي رب من هذا ؟ فقال هذا رجل من آخر الأمم من ذريتك يقتل له داود فقال : رب كم جعلت عمره ؟ قال ستين سنة قال أي رب زده من عمري أربعون سنة فلما قضي عمر آدم جاءه ملك الموت فقال أولم يبق من عمري أربعون سنة ؟ أولم تعطها أبنك داود ؟ قال فجحد آدم فجحدت ذريته و نسي آدم فنسيت ذريته و خطىء آدم فخطءت ذريته . هذا حديث حسن صحيح و قد روي من غير وجه عن أبي هريرة عن النبي صلى الله عليه و سلم

3076. At-Tirmidhi ya rubuto daga Abu Hurairata wanda yace, Manzon Allah SAW ya ce: "Lokacin da Allah Ya halitta Adam sai Ya shafa gadan bayan Adam sai ga duk waɗanda Allah zai halittasu har zuwa Ranar ƙiyama sun fito daga tsatson Adam, sai Allah Ya sanya Wani Haske a goshin kowannensu sannan Ya bijirosu ga Adam. Sai Adam ya tambaya

"Ya Ubangijina su waye waɗannan?" Allah Ya ce 'ya'yanka ne. Sai Adam ganin wani da Hasken goshinsa ya ƙayatar da shi ya ce "Ya Ubangijina wane wanna?" Sai Allah Ya ce masa wannan na daga cikin 'ya'yanka na ƙarshe-karshen zamani mai suna Dawud. Sai Adam ya tambaya "Ya Ubangijina tsahon shekaru nawa Ka ƙaddara masa?" Sai Allah Ya ce shekara sittin, sai Adam ya ce "Ya Ubangijina ƙara masa arba'in daga shekarun da Ka ƙaddara mini".

Lokacin da shekarun Adam suka kusa karewa sai Mala'ikan Mutuwa ya zo masa, sai Adam ya ce "Ba inada sauran shekaru arba'in (da zan ƙarasa) ba"? Sai Mala"ikan Mutuwa ya ce "ba ka baiwa ɗanka Dawud su ba?" Sai ya ce; Adam yayi musunsu, saboda haka 'ya'yansa suke da musu, Adam ya manta haka 'ya'yansa suke da mantuwa, Adam ya yi sabo shi yasa 'ya'yansa suke yin sabo. Wannan Hadithi Hasan Sahih ne daga cikin littafin At-Tirmidhi babin Tafsirin Alƙur'ani - Surah A'araf Hadithi na 3076.

حدثنا عبد الله بن محمد حدثنا عبد الرزاق عن معمر عن همام عن أبي هريرة رضي الله عنه عن النبي صلى الله عليه و سلم قال خلق الله آدم و طوله ستون ذراعا ثم قال اذهب فسلم على أولاءك من الملائكة فاستمع ما يحيونك تحيتك و تحية ذريتك فقال السلام عليكم فقالوا السلام عليك و رحمة الله فزادوه و رحمة الله فكل من يدخل الجنة على صورة آدم فلم يزل الخلق ينقص حتى الأن

3326. Al-Bukhari ya rubuto daga Abu Hurairah cewar Manzon Allah SAW ya ce: Allah Ya halicci Adam tsahon zira'i sittin. Sai ya ce jeka ka yiwa wadancan taron Mala'ikun gaisuwa ta sallama, kuma ka saurari amsar da za su baka, domin wannan ya zama gaisuwarka da zuriyarka. Sai ya ce musu "Assalamu alaikum" sai suka amsa masa da "Assalamu alaika wa rahmatullahi". Sun ƙara wa rahmatullahi. Duk waɗanda za su shiga Aljanna za su shiga ne da girman zira'i sittin. Amma tsahon da

girman ɗan Adam bai daina raguwa ba tun daga farkon yayan Adam har zuwa yanzu. Al-Bukhari: Littafin Haddithin Annabawa.

حدثنا قيس بن حفص حدثنا خالد بن الحارث حدثنا شعبة عن أبي عمران الجوني عن أنس يرفعه أن الله يقول لأهون أهل النار عذابا لو أن لك ما في الأرض من شيء كنت تفتدي به قال نعم قال فقد سألتك ما هو أهون من هذا و أنت في صلب آدم أن لا تشرك بي فأبيت إلا الشرك

3334. Anas bin Malik ya faɗa cewar Annabi ya ce "Allah zai cewa wani daga cikin yan Wuta "Da ace duk abinda ke cikin ƙasa (na arziki) naka ne shin za ka fanshi kanka da shi daga wannan azabar Wutar?" Sai yace ƙwarai kuwa. Sai Ya ce (Allah) Na nemi abinda yafi wannan sauƙi lokacin da Na karɓi alkawarin ka sa'ad da kake tsatson babanka Adamu cewar ba za kayi shirka ba cikin bauta Mini amma ka doge sai shirkar kawai. Bukhari.

4) FARKON KAUCEWAR ƊAN ADAM DAGA KAN ADDINI ƊAYA KWAL MAI ƊAUKE DA TSANTSAR TAUHIDI.

Kamar yadda muka karanta nan baya cewar Allah SWT Ya fitar da Annabi Adamu Alaihis Salaam (AS) da matarsa Hauwa'u daga Aljanna zuwa Duniya tare da Iblis watau Shaiɗan, cewa dai duk wanda yabi ShiriyarSa ta hanyar Manzanni ya kuɓuta daga sharrin Shaiɗan. Sai ya kasance duk rãyuwar Annabi Adamu kafin ya rasu a nan Duniya tare da 'ya'yansa suna kan Tauhidi tsantsa kamar yadda Allah SWT Ya umarcesu. Annabi Adamu ya rayu shekara ɗari tara da sittin sannan tsakaninsa da farkon Manzon da aka fara aikowa ga 'ya'yansa watau Annabi Nuhu AS, ƙarni goma ne watau shekara dubu. A cikin wannan shekaru dubun, bayan rasuwar Annabi Adamu, 'ya'yansa suka jirkita

Addinin gaskiya mai ɗauke da Tsantsar Tauhidi suka koma bautawa gumaka da Shehunnai.

Yadda abin yake shine; daga cikin 'ya'yan Annabi Adamu akwai manyan masu tsoron Allah tare da kyautatawa da yawan bautarsu ga Allah SWT. Sunayen wasunsu akwai kamar haka; Wadda, Suwa'a, Yagusa, Ya'uƙa da Nasra.

Bayan iri-irin waɗannan manyan Shehunnai (Wadda da Suwa'a da sauransu) sun rasu, sai ilimin Addinin bautawa Allah Shi kaɗai (Tauhidi) yayi rauni. Bayan wasu ƙarnoni daga cikin ƙarni goman can (kafin aiko Annabi Nuhu), sai Jama'a suka fara shauƙin waɗancan manyan malamai da suka rasu (ta hanyar karanta tarihinsu). Daga nan sai Iblis ya riya musu cewar mai zai sa ba za su yi mutun-mutuminsu ba domin ko yaushe suka ga gumakansu sai su tuna dasu sannan hankalinsu ya kwanta? Suka karɓi shawarar Iblis. Bayan waɗanda suka yi gumakan waɗancan Shehunnai sun rasu sai Iblis ya sake ziyartar na bayansu ya ce musu; "kun ga waɗannan gumakanfa da kuke gani a guraren Ibadarku, mutanen da suka gabaceku (kakannin kakanninku) bauta musu suke yi. Shikenan sai bautar Allah ta shuɗe, aka koma bautawa gumaka. Saboda Rahamar Allah ga 'ya'yan Adamu, bai barsu haka kan Shirka da kafirci ba, sai Ya aiko musu da Manzon Farko Annabi Nuhu AS domin komawa ga Addini ɗaya na Tauhidi.

Lokacin da Annabi Nuhu AS yake ta wa'azi domin komawa ga Tauhidi, shin duk Jama'arsa sun karbi kiransa domin koma kan Addini ɗaya ƙwal? A'a sai yan kaɗan. Shi ya sanya Allah Ya umarce shi da sassaka jirgin ruwa wadda zai dauke shi da ragowar waɗanda suka yi Imani da abinda aka aiko musu na Tauhidi da sauran dabbobi nau'i bibbiyu. Sannan Ya aiko da ruwan ɗufana wanda ya halakar da kangararru kuma Ya

tseratar da Annabi Nuhu da mutanen da suka yi Imani da shi ta hanyar babban jirgin ruwan da ya ɗebesu.

Mu sani Iblis ɗan tawaye shugaban mahassada da kangararru, kuma maƙiyin banu Adama yana nan har yau, kuma yayi Alƙawarin halakar da 'yan Adam. Wannan kuwa a baiyane yake ta yadda har yau akwai masu bautawa Shehunnai da hotunansu a cikin Al'ummar Musulmai a wannan ƙasa tamu.

Abin farin cikin shine, Allah Mai Rahama da Gafara ga bayinSa Yana nan, Shi kuma har bayan gobe, sannan Yayi Alƙawarin kare bayinSa na gari daga Sharrin Shaiɗan. Shi yasa har kullum sai an sami masu kare Tauhidi, in sha Allah.

4.1 HUJJA DAGA ALKUR'ANI

4.1.1 KASANCEWAR AL'UMMA ƊAYA KAN ADDINI ƊAYA TUN ASALI.

وما كان الناس إلا أمة واحدة فاختلفوا ولولا كلمة سبقت من ربك لقضي بينهم فيما فيه يختلفون

"Kuma mutãne ba su kasance ba fãce Al'umma guda (kan Addini guda ɗaya Tilo), sa'an nan kuma suka sãɓãwa jũna, kuma ba dõmin wata kalma ba wadda ta gabãta daga Ubangijinka, dã anyi hukunci a tsakãninsu a kan abinda yake a cikinsa wadda suka sãɓãwa jũna." Surah Yunus aya ta 19.

كان الناس أمة واحدة فبعث الله النبيين مبشرين و منذرين و أنزل معهم الكتاب بالحق ليحكم بين الناس فيما اختلفوا فيه وما اختلف فيه إلا الذين أوتوه من بعد ما جاءتهم البينات بغيا بينهم فهدى الله الذين ءامنوا لما اختلفوا فيه من الحق بإذنه والله يهدي من يشاء إلى صراط مستقيم

"Mutãne sun kasance al'umma guda ɗaya. (Da suka rarrabu) Sai Allah Ya aiki annabãwa suna mãsu bãyar da bishãra kuma mãsu gargaɗi; kuma Ya saukar da Littãfi da gaskiya tãre da su dõmin (Littãfin) ya yi hukunci a tsakãnin mutãnen a cikin abinda suka sãɓãwa jũna a cikinsa. kuma bãbu wanda ya sãɓã, a cikinsa, fãce waɗanda aka baiwa shi daga bãyan hujjõji bayyanannu sun je musu dõmin zãlunci a tsakãninsu. Sai Allah Ya shiryar da waɗanda suka yi ĩmani ga abinda suka sãɓã a cikinsa daga gaskiya da izninSa. Kuma Allah Yana shiryar da wanda Yake so, zuwa ga hanya madaidaiciya." Surah Al-Baqarah aya ta 213.

4.1.2 TAWAYEN IBLIS - MAI RUDIN JAMA'A DON SU RARRABA SU YI GABA DA JUNANSU.

و إذ قلنا للملائكة اسجدوا لآدم فسجدوا إلا إبليس أبى و استكبر و كان من الكافرين

Kuma a lõkacin da Muka ce ga malã'iku: "Ku yi sujada ga Ãdam," Sai suka yi sujada, fãce Ibilĩsa ya ƙi, kuma ya yi girman kai, kuma ya kasance daga kãfirai. Surah Al-Baqarah aya ta 34.

قال ما منعك ألا تسجد إذ أمرتك قال أنا خير منه خلقتني من نار و خلقته من طين

"Ya ce: "Mẽne ne ya hana ka, ba ka yi sujada ba, alõkacin da Na umurce ka?" Ya ce: "Nĩ ne mafĩfĩci daga gare shi, Ka halitta ni daga wuta alhãli kuwa Kã halitta shi daga lãka." Surah Al-Aʿraf aya ta 12.

و إذ قلنا للملائكة اسجدوا لآدم فسجدوا إلا إبليس كان من الجن ففسق عن أمر ربه أفتتخذونه و ذريته أولياء من دوني و هم لكم عدو بأس للظالمين بدلا

Kuma a lõkacin da Muka ce wa malãiku, "Ku yi sujada ga Ãdamu." Sai suka yi sujada fãce Iblĩsa, yã kasance daga aljannu sai ya yi fãsiƙanci ga barin umurnin Ubangijinsa, To fa, ashe, kunã riƙon sa, shi da zũriyarsa,

su zama majiɓinta baicin Ni, alhãli kuwa su maƙiya ne a gare ku? Tir da ya zama musanya ga azzãlumai." Surah Al-Kahf aya ta 50.

و إذ قلنا للملائكة اسجدوا لآدم فسجدوا إلا إبليس قال ءأسجد لمن خلقت طينا

قال أرءيتك هذا الذي كرمت علي لإن أخرتن إلى يوم القيامة لأحتنكن ذريته إلا قليلا

قال اذهب فمن تبعك منهم فإن جهنم جزاؤكم جزاء موفورا

واستفزز من استطعت منهم بصوتك و أجلب عليهم بخيلك ورجلك وشاركهم في الأموال و الأولاد و عدهم وما يعدهم الشيطان إلا غرورا

إن عبادي ليس لك عليهم سلطان و كفى بربك وكيلا

"Kuma a lõkacin da Muka cẽ wa malã'iku, "Ku yi sujada ga Ãdamu," sai suka yi sujada, fãce Ibilĩsa, ya ce: "shin, zan yi sujada ga wanda ka halitta shi yanã lãka?"

"Ya ce: "Shin, kã ganKa wannan wanda Ka girmama a kaina, lalle ne idan Ka jinkirtã mini zuwa ga Rãnar Kiyãma lalle ne, zan tumɓuke zuriyarsa, fãce kaɗan."

"Ya ce: "Ka tafi. Sa'an nan wanda ya bĩ ka daga gare su, to, Jahannama ce sakamakonku, (Mu ba ku shi) sakamako cikakke."

"Kuma ka rikitar da wanda ka sãmi ĩko a kansa, daga gare su, da sautinka, kuma ka yi hari a kansu da dawãkinka da dãkãrunka kuma ka yi tãrẽwa da su a cikin dũkiyõyi da ɗiyã, kuma ka yi musu wa'adi. Alhãli kuwa Shaiɗan bã ya yi musu wa'adin kõme fãce da ruɗi."

"Lalle ne bãyiNa, bã ka da wani ƙarfi a kansu. Kuma Ubangijinka Ya isa Ya zama Wakĩli." Surah Al-Israʾi aya ta 61 zuwa ta 65.

إن الشيطان لكم عدو فاتخذوه عدوا إنما يدعوا حزبه ليكونوا من أصحاب السعير

Lalle Shaiɗan maƙiyi ne a gare ku, sai ku riƙe shi maƙiyi. Yanã kiran ƙungiyarsa kawai ne, dõmin su kasance 'yan Wutar sa'ira." Surah Fāṭir aya ta 6

4.1.3 ALKAWARIN ALLAH

ألم أعهد إليكم يابني ءادم أن لا تعبدوا الشيطان إنه لكم عدو مبين

"Ashe, ban yi muku umurni na alkawari ba, yã ɗiyan Ãdamu? Cẽwa kada ku bauta wa Shaiɗan, lalle shĩ, maƙiyi ne a gareku bayyananne?" Surah Ya-Sin aya ta 60.

و الذين ءامنوا بالله و رسله أولاءك هم الصديقون والشهداء عند ربهم لهم أجرهم و نورهم و الذين كفروا و كذبوا بآياتنا أولاءك أصحاب الجحيم

Kuma waɗanda suka yi ĩmãni da Allah da MazanninSa waɗannan sũne kamãlar gaskatãwa kuma sune mãsu shahãda a wurin Ubangjinsu. Sunã da sakamakonsu da haskensu. Waɗanda suka kafirta kuma suka ƙaryata game da ãyõyinMu, waɗannan sune 'yan Wutar Jahĩm. Surah Al-Ḥadid aya ta19.

و للذين كفروا بربهم عذاب جهنم و بإس المصير

Kuma waɗanda suka kafircewa Ubangjinsu na da azãbar Jahannama, tã munana ga zamanta makõmarsu." Surah Al-Mulk aya ta 6.

4.1.4 AIKO ANNABI NUHU, TSERATAR DA SHI TARE DA WAƊANDA SUKA YI IMANI DA SHI, DA HALAKA KAFIRAN ZAMANINSA.

و إن ربك لذو فضل على الناس و لاكن أكثرهم لا يشكرون

Kuma lalle ne Ubangijinka, haƙĩƙa Mai falala ne a kan mutãne kuma amma mafi yawansu, bã su gõdẽwa. Surah An-Naml aya ta 73.

إنا أرسلنا نوحا إلى قومه أن أنذر قومك من قبل أن يأتيهم عذاب أليم

Lalle ne Mun aiki Nũhu zuwa ga mutãnensa, cẽwa ka yi gargaɗi ga mutãnenka gabãnin wata azãba mai raɗaɗi ta zo musu. Surah Nuh aya ta 1.

و قالوا لا تذرن ءالهتكم و لا تذرن ودا و لا سواعا و لا يغوث و يعوق و نسرا

Kuma suka ce: Faufau kada ku bar gumãkanku, kuma faufau, kada ku bar wadda, kuma kada ku bar suwã kuma kada ku bar Yagũsa da Ya'uƙa da Nasra." Surah Nuh aya ta 23. Duba Tafsirin Qurdabi akan wannan ayar.

واصنع الفلك بأعيننا و وحينا و لا تخاطبني في الذين ظلموا إنهم مغرقون

و يصنع الفلك و كلما مر عليه ملأمن قومه سخروا منه قال إن تسخروا منا فإنا نسخر منكم كما تسخرون

فسوف تعلمون من يأتيه عذاب يخزيه و يحل عليه عذاب مقيم

حتى إذا جاء أمرنا و فار التنور قلنا احمل فيها من كل زوجين اثنين و أهلك إلا من سبق عليه القول و من ءامن و ما ءامن معه إلا قليل

"Kuma ka sassaƙa jirgi da kyau a kan idanunMu da wahayinMu, kuma kada ka yi Mini magana a cikin sha'anin waɗanda suka kãfirta, lalle ne sũ, waɗanda ake nutsarwa ne."

"Kuma Yanã sassaƙa jirgin cikin natsuwa, kuma a kõ yaushe waɗansu shugabanni daga mutãnen sa suka shũɗe a gaban sa, sai su yi izgili gare shi. Ya ce: "Idan kun yi izgili gare mu, to, haƙĩƙa mũ mã zã mu yi izgili gare ku, kamar yadda kuke yin izgili."

"Sa'an nan da sannu zã ku san wanda azãba zã ta zo masa, ta wulakantã shi (a dũniya), kuma wata azãba zaunanna ta sauka a kansa (a Lãhira)."

"Har a lõkacin da umurninMu ya je, kuma tandã ta ɓulɓula. Muka ce: "Ka ɗauka, a cikinta (jirgin ruwan), daga kõme, ma'aura biyu, da kuma iyalanka, fãce wanda magana ta gabãta a kansa*, da wanda ya yi ĩmãni." Amma kuma bãbu waɗanda suka yi ĩmãni tãre da shi fãce kaɗan." Surah Hud aya ta 37-40.

4.2 HUJJA DAGA AHADITH

Abdullahi Ibn Abbas ya ce "tsakanin Adam da Nuh akwai ƙarni goma watau shekara dubu, lokacin da kowa yake bin addinin Musulunci (Mika wuya ga dokokin Allah SWT). Daga Hakim

Al-Hafiz Abu Hatin Ibn Hibban ya ce a cikin Saheeh ɗinsa: daga Abu Umamah wanda ya ce: wani mutum ya tambayi Manzon Allah SAW: "Ya Manzon Allah shin Adam Annabi ne?" Manzon Allah SAW yace "E, kuma Allah Ya yi masa magana". Mutumin ya sake tambaya: "To shekaru nawa ne tsakaninsa da (Annabi) Nuhu?" Annabi ya amsa masa: "ƙarni goma". Daga ibnu Hibban.

5) AIKO SAURAN MANZANNI DON KOMAWA KAN TAFARKIN ASALI NA TAUHIDI.

5.1 HUJJA DAGA ALKUR'ANI

و تلك حجتنا ءاتيناها إبراهيم على قومه نرفع درجات من نشاء إن ربك حكيم عليم

و وهبنا له إسحاق و يعقوب كلا هدينا و نوحا هدينا من قبل و من ذريته داود و سليمان و أيوب و يوسف و موسى و هارون و كذلك نجزى المحسنين

و زكريا و يحيى و عيسى و إلياس كل من الصالحين

و إسماعيل و اليسع و يونس و لوطا و كلا فضلنا على العالمين

و من ءاباءهم و إخوانهم و اجتبيناهم و هديناهم إلى صراط مستقيم

ذلك هدى الله يهدي به من يشاء من عباده ولو أشركوا لحبط عنهم ما كانوا يعملون

أولاءك الذين ءاتيناهم الكتاب و الحكم و النبوة فإن يكفر بها هاؤلاءفقد وكلنا بها قوما ليسوا بها بكافرين

أولاءك الذين هدى الله فبهداهم اقتده قل لا أسألكم عليه أجرا إن هو إلا ذكرى للعلمين

Kuma waccan ita ce hujjar Mu, Mun bayãr da ita ga Ibrãhĩma (Abraham)a kan mutãnensa. Munã ɗaukaka wanda Muka so da darajõji. Lalle ne Ubangijinka Mai hikima ne, Masani.

Kuma Muka bã shi Is'hãƙa (Isaaq) da Yãƙubu (Jacob), dukansu Mun shiryar, kuma Nũhu (Noah) Mun shiryar da shi a gabãni, kuma daga zuriyarsa akwai Dãwũda (David) da Sulaimãnu (Solomon) da Ayyũba (Job), da Yũsufu (Joseph) da Mũsã (Moses) da Hãrũna (Aaron), kuma kamar wancan ne Muke sãka wa mãsu kyautatãwa.

Da Zakariyya (Zechariah) da Yahaya (John) da Isa (Jesus) da Ilyasu (Elias)dukansu daga sãlihai suke.

Da Ismã'la (Ishmael) da Ilyasa (Elisha), da Yũnusa (Jonah) da Luɗu (Lot), kuma dukansu Mun fĩfĩtã su a kan tãlikai.

Kuma daga ubanninsu, da zũriyarsu, da 'yan'uwansu, kuma Muka zãɓe su, kuma Muka shiryar da su zuwa ga hanya madaidaiciya.

Wancan ne shiryarwar Allah, Yanã shiryar da wanda Yake so daga bayinSa. Kuma dã sun yi shirki dã haƙĩƙa abin da suka kasance sunã, aikatãwa yã lãlãce.

Waɗancan ne waɗanda Muka bai wa Littãfi da hukunci da Annabci. To idan waɗannan (mutãne) sun kãfirta da ita, to, haƙĩƙa, Mun wakkala wasu mutãne gare ta, ba su zama game da ita kãfirai ba.

Waɗancan ne Allah Ya shiryar, sabõda haka ka yi kõyi da shiryarsu. Ka ce: "Ba ni tambayar ku wata ijãra. Shĩ (Alƙur'ãni) bai zama ba fãce tunãtarwa ga tãlikai." Surah Al-Anʿam aya ta 83 zuwa ta 90.

تلك الرسل فضلنا بعضهم على بعض منهم من كلم الله و رفع بعضهم درجات و ءاتينا عيسى ابن مريم البينات و أيدناه يروح القدس ولو شاء الله ما اقتتل الذين من بعدهم من بعد ما جاءتهم البينات و لاكن اختلفوا فمنهم من ءامن و منهم من كفر ولو شاء الله ما اقتتلوا و لاكن الله يفعل ما يريد

"Waɗancan manzannin Mun fĩfĩta sãshensu a kan sãshe: Daga cikinsu akwai wanda Allah Ya yi masa magana; kuma Ya ɗaukaka sãshensu da darajõji; kuma Muka bai wa Ĩsã dan Maryama hujjõji bayyanannu, kuma Muka ƙarfafã shi da Rũhi mai tsarki. Kuma dã Allah Yã so dã waɗanda suke daga bãyansu, bã zã su yi yãƙi ba, daga bãyan hujjõji bayyanannu sun je musu. Kuma amma sun sãɓawa jũna, sabõda haka daga cikinsu akwai wanda ya yi ĩmãni, kuma daga cikin su akwai wanda ya kãfirta. Kuma dã Allah Yã so dã bã zã su yãƙi jũna ba, kuma amma Allah Yana aikata abinda Yake nufi." Surah Al-Baqarah aya ta 253.

لا إكراه في الدين قد تبين الرشد من الغي فمن يكفر بالطاغوت و يؤمن بالله فقد استمسك بالعروة الوثقى لا انفصام لها و الله سميع عليم

"Bãbu tĩlastãwa a cikin addini, haƙĩƙa shiriya tã bayyana daga ɓata; Sabõda haka wanda ya kãfirta da dãgũta kuma ya yi ĩmãni da Allah, to, haƙĩƙa, yã yi riƙo ِga igiya amintacciya, bãbu yankẽwa agare ta. Kuma Allah Mai ji ne, Masani." Surah Al-Baqarah aya ta 256.

Al'A'araf 59-64, Yunus 71-72, Saffat 75-81, Taubat 70, Isra'i 3 & 17, Qaf 12-14, At-Tahreem 10,

5.2 HUJJA DAGA AHADITH

حدثنا محمد بن كثير أخبرنا سفيان عن منصور عن إبراهيم عن عبيدة عن عبد الله رضي الله عنه عن النبي صلى الله عليه و سلم قال خير الناس قرني ثم الذين يلونهم ثم الذين يلونهم ثم يجيء أقوام تسبق شهادة أحدهم يمينه و يمينه شهادته قال إبراهم و كانوا يضربوننا على السعادة والعهد

2669. 'Abdullãh RA ya ce: Manzon Allah SAW ya ce: Mafi alkhairin mutane sune na wannan karnin da nake ciki, sai ƙarni mabiyansa, sai ƙarni mabiyansa. Bayan Waɗannan wasu mutane za su baiyana waɗanda shaidar su za ta rigayi rantsuwarsu, kuma rantsuwarsu ta rigayi shaidar su."

Duba Muslim (2533), At-Tirmidhi (3859). Ibn Majah (2362) and Ahmad (3583), daga Abdullah Ibn Mas'ood.

6. AIKO MANZON KARSHE, CIKAMAKIN ANNABAWA, SHUGABAN MANZANNI, MUHAMMAD SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA (SAW).

Allah SWT cikin RahamarSa bayan waɗancan Manzanni sun shude kuma Addinin Gaskiya ya dada gurbacewa ta hanyar yi masa cushe da Shirka nau'i - nau'i da sabo maras ma'ana cikin Siffar Allah da IkonSa, sai Ya aiko da Muhammadu SAW a matsayin Manzon ƙarshe watau Cikamakin Annabawa kuma Shugaban Manzanni.

"Muhammadu bai kasance uban kõwa ba daga mazanku, kuma amma shĩ yã kasance Manzon Allah kuma cikon Annabãwa (na ƙarshensu). Kuma Allah Ya kasance Masani ga kõme." Surah Al-Ahzāb aya ta 40.

"Kuma bã ya yin magana daga son zuciyarsa."

"(Maganarsa) ba ta zamo ba, fãce wahayi ne da ake aikõwa." Surah An-Najm aya ta 3 da ta 4.

قل ما كنت بدعا من الرسل و ما أدرى ما يفعل بى و لا بكم إن أتبع إلا ما يوحى إلي و ما أنا إلا نذير مبين

Ka ce: "Ban kasance fãrau ba daga Manzanni, kuma ban san abinda zã a yi game da ni kõ game da ku (na gaibi) ba, bã ni bin kõme fãce abinda ake yin wahayi zuwa gare ni, kuma ban zama ba, fãce mai gargaɗi mai bayyanãwa." Surah Al-Aḥqaf aya ta 9.

و كذلك أوحينا إليك روحا من أمرنا ما كنت تدري ما الكتاب و لا الإيمان و لاكن جعلناه نورا نهدي به من نشاء من عبادنا و إنك لتهدي إلى صراط مستقيم

صراط الله الذي له ما في السماوات و ما في الأرض ألا إلى الله تصير الأمور

Kuma kamar wancan Mun aika wani rũhi (rai mai haɗa jama'a) zuwa gare ka, daga gare Mu. Ba ka kasance kã san abinda yake littãfi ba, kõ

abinda Yake ĩmãni, kuma amma Mun sanya shi (rũhin, watau Alƙur'ãni) wani haske ne, Munã shiryar da wanda Muke so daga cikin bãyĩnMu game da shi. Kuma Lalle kai, haƙĩƙa, kanã shiryarwa zuwa ga hanya, madaidaiciya.

Hanyar Allah wanda ke da mulkin abinda ke cikin sammai da abinda ke cikin ƙasa. To, zuwa ga Allah kawai al'amura ke kõmãwa. Surah Ash-Shura aya ta 52 da 53.

فإن حآجوك فقل أسلمت وجهي لله و من اتبعن و قل للذين أوتوا الكتاب و الأميين ءأسلمتم فإن أسلموا فقد اهتدوا و إن تولوا فإنما عليك البلاغ والله بصير بالعباد

إن الذين يكفرون بآيات الله و يقتلون النبيين بغير حق و يقتلون الذين يأمرون بالقسط من الناس فبشرهم بعذاب أليم

أولاءك الذين حبطت أعمالهم في الدنيا و الآخرة و ما لهم من ناصرين

"To, idan sun yi musu da kai, sai ka ce: "Nã sallama fuskata ga Allah, kuma wanda ya bi ni (haka)." Kuma ka ce wa waɗanda aka baiwa littãfi (Yahudu da Kirista) da Ummiyyai (Maguzawa): "Shin kun sallama?" To, idan sun sallama, haƙĩƙa, sun shiryu kuma idan sun jũya, to kawai abinda ke kanka, shi ne iyarwa. Kuma Allah Mai gani ne ga bãyinSa."

"Lalle ne waɗanda suke kãfirta da ãyõyin Allah, kuma suna kashe Annabãwa bã da wani hakki ba, kuma suna kashe waɗanda ke umurni da yin ãdalci daga mutãne, to ka yi musu bushãra da azãba mai raɗaɗi".

"Waɗannan ne waɗanda ayyukansu suka ɓãci a cikin dũniya da Lãhira, kuma bã su da wasu mataimaka." Surah Ali-ʿImran aya ta 20 zuwa ta 22

و بالحق أنزلناه و بالحق نزل و ما أرسلناك إلا مبشرا و نذيرا

و قرءانا فرقناه لتقرأه على الناس على مكث و نزلناه تنزيلا

قل ءامنوا به أو لا تؤمنوا إن الذين أوتوا العلم من قبله إذا يتلى عليهم يخرون للأذان سجدا

و يقولون سبحان ربنا إن كان وعد ربنا لمفعولا

و يخرون للأذقان يبكون و يزيدهم خشوعا

قل ادعوا الله أو ادعوا الرحمان أيا ما تدعوا فله الأسماء الحسنى و لا تجهر بصلاتك و لا تخافت بها و ابتغ بين ذالك سبيلا

و قل الحمد لله الذي لم يتخذ ولدا و لم يكن له شريك في الملك و لم يكن له ولي من الذل و كبره تكبيرا

Kuma da gaskiya Muka saukar da shi, kuma da gaskiya ya sauka. Kuma ba Mu aike ka ba fãce kanã mai bãyar da bushãra kuma mai gargaɗi.

Kuma yanã abin karãtu Mun rarraba shi dõmin ka karanta shi ga mutane a kan jinkiri kuma Mun sassaukar da shi sassaukarwa.

Ka ce: "Ku yi ĩmãni da Shi, ko kuwa kada ku yi ĩmãni, lalle ne waɗanda aka bai wa ilmi daga gabãninsa, idan anã karãtunsa a kansu, sunã fãɗuwa ga haɓõɓinsu, sunã mãsu sujada."

"Kuma sunã cẽwa: Tsarki ya tabbata ga Ubangijinmu! Lalle ne wa'adin Ubangijinmu ya kasance, haƙĩƙa, abin aikatãwa."

Kuma sunã fãɗuwa ga haɓõɓinsu sunã kũka, kuma yanã ƙara musu tsõro.

Ka ce: "Ku kirayi Allah kõ kuwa ku kirãyi Mai rahama. Kõwane kuka kira to Yanã da sũnãye mafi kyau. Kuma, kada ka bayyana** ga sallarka, kuma kada ka ɓõye ta. Ka nẽmi hanya a tsakãnin wancan."

Kuma ka ce: "Gõdiyã (haɗe da yabo) ta tabbata ga Allah wanda bai riƙi ɗã ba kuma abõkin tãrayya bai kasance a gare Shi ba a cikin mulkinSa, kuma (ba shi da buƙata ga) wani masõyi (mai bashi Shi kariya) sabõda gajiyawarSa." Kuma ka girmama Shi, girmamãwa. Surah Al-Israi aya ta 105 ZUWA ta 111

6.1. JAN HANKALIN MUSULMAN WANNAN ZAMANI DA MASU ZUWA NAN GABA.

يا أيها الذين ءامنوا لا تتخذوا الكافرين أولياء من دون المؤمنين أتريدون أن تجعلوا لله عليكم سلطانا مبينا

إن المنافقين في الدرك الأسفل من النار و لن تجد لهم نصيرا

إلا الذين تابوا و أصلحوا و اعتصموا بالله و أخلصوا دينهم لله فألاءك مع المؤمنين و سوف يؤت الله المؤمنين أجرا عظيما

Yã ku waɗanda suka yi ĩmãni! Kada ku riƙi kãfirai masõya, baicin mũminai. Shin, kunã nufin ku sanyãwa Allah dalĩli bayyananne a kanku?"

"Lalle ne, manãfukai sunã a magangara mafi ƙasƙanci daga wuta. Kuma bã zã ka sãma musu mataimaki ba."

"Sai waɗanda suka tũba, kuma suka gyãra, kuma suka nẽmi kafuwa ga Allah, kuma suka tsarkake addininsu dõmin Allah, to, waɗannan sunã tãre da mũminai, kuma Allah zai bai wa mũminai lãda mai girma." Surah An-Nisaʾ aya ta 144 zuwa ta 146.

و ما اختلفتم فيه من شيء فحكمه إلى الله ذلكم الله ربي عليه توكلت و إليه أنيب

Kuma abinda kuka sãɓã wa jũna a cikinsa kõ mêne ne, to, hukuncinsa (a mayar da shi) zuwa ga Allah. Wancan Shĩ ne Allah Ubangijĩna, a gare Shi na dõgara, kuma zuwa gare Shi nake mayar da al'amarĩna. Surah Ash-Shura aya ta 10.

يآ أيها الذين ءامنوا أطيعوا الله و أطيعوا الرسول و أولي الأمر منكم فإن تنازعتم في شيء فردوه إلى الله و الرسول إن كنتم تؤمنون بالله و اليوم الآخر ذالك خير و أحسن تأويلا

"Yã kũ waɗanda suka yi ĩmãni! Ku yi ɗã'a ga Allah, kuma ku yi ɗã'a ga ManzonSa, da ma'abũta al'amari daga cikinku (shugabanni masu tsoron Allah). Idan kun yi jãyayya a cikin wani abu, to ku mayar da shi zuwa ga Allah da ManzonSa (Alkur'ani da Sunnah) idan kun kasance kunã ĩmãni da Allah da Rãnar Lãhira. wannan ne mafi alhẽri, kuma mafi kyau ga fassara" Surah An-Nisaʾ aya ta 59.

فلا و ربك لا يؤمنون حتى يحكموك فيما شجر بينهم ثم لا يجدوا في أنفسهم حرجا مما قضيت و يسلموا تسليما

To, a'aha! Ina (Ni Allah) rantsuwa da Ubangijinka, ba za su yi ĩmãni ba, sai sun yarda da hukuncinka (Ya Muhammad) ga abinda ya sãɓa a tsakãninsu, sa'an nan kuma ba su sãmi wani ƙunci a cikin zukãtansu ba, daga abinda ka hukunta, kuma su sallama sallamãwa. Surah An-Nisaʾ aya ta 65.

Allah SWT Yana Jan kunnenmu cikin waɗannan ayoyi cewar idan mu Musulmi mun saba cikin duk wani al'amari, to mu koma ga Hukuncin Allah dake cikin Alkur'ani Mai Tsarki, da Sunnar ManzonSa domin rashin fahimta ko jayayya ko sabanin ya gushe, a dunkule a zama cikin bin Alkibla guda wadda babu karkata cikinta.

و اعتصموا بحبل الله جميعا و لا تفرقوا و اذكروا نعمت الله عليكم إذ كنتم أعداء فألف بين قلوبكم فأصبحتم بنعمته إخوانا و كنتم على شفاحفرة من النار فأنقذكم منها كذالك يبين الله لكم ءاياته لعلكم تهتدون

و لتكن منكم أمة يدعون إلى الخير و يأمرون بالمعروف و ينهون عن المنكر و أولاءك هم المفلحون

و لا تكونوا كالذين تفرقوا و اختلفوا من بعد ما جاءهم البينات و أولاءك لهم عذاب عظيم

"Kuma ku yi daidami da igiyar Allah gabã ɗaya, kuma kada ku rarraba. Kuma ku tuna ni'imar Allah a kanku a lõkacin da kuka kasance maƙiya sai Ya sanya sõyayya a tsakãnin zukãtanku sabõda haka kuka wãyi gari, da ni'imarSa, 'yan'uwa. Kuma kun kasance a kan gãɓar rãmi na wutã sai Ya tsãmar da ku daga gare ta, Kamar wannan ne Allah Yake bayyana muku ayõyinSa, tsammãninku, zã ku shiryu".

"Kuma wata jama'a daga cikinku, su kasance suna kira zuwa ga alhẽri, kuma suna umurni da alhẽri, kuma suna hani daga abinda ake ƙi (sabo, fasikanci, zalunci da Shirka). Kuma waɗannan, sũne mãsu cin nasara."

"Kuma kada ku kasance kamar waɗanda suka rarrabu kuma suka sãɓã wa jũna, bãyan hujjõji bayyanannu sun je musu kuma waɗannan sunã da azãba mai girma." Surah Ali-ʿImran aya ta 103 zuwa ta 105.

6.2. UMARNI GA MANZON WANNAN ZAMANIN HAR ZUWA RANAR TASHIN KIYAMA.

و أنزلنا أليك الكتاب بالحق مصدقا لما بين يديه من الكتاب و مهيمنا عليه فأحكم بينهم بما أنزل الله و لا تتبع أهواءهم عما جاءك من الحق لكل جعلنا منكم سرعة و منهاجا ولو شاء الله لجعلكم أمة واحدة و لاكن ليبلوكم في ما ءاتاكم فاستبقوا الخيرات إلى الله مرجعكم جميعا فينبأكم بما كنتم فيه تختلفون

و أن احكم بينهم بما بما أنزل الله و لا تتبع أهواءهم و احذرهم أن يفتنوك عن بعض ما أنزل الله إليك فإن تولوا فاعلم أنما يريد الله أن يصيبهم ببعض ذنوبهم و إن كثيرا من الناس لفاسقون

أفحكم الجاهلية يبغون و من أحسن من الله حكما لقوم يوقنون

"Kuma Mun saukar da Littãfi zuwa gare ka (Ya Muhammad) da gaskiya, yanã mai gaskatãwa ga abinda yake a gaba gare shi daga Littãfi (Attaura da Injĩla), kuma mai halartãwa a kansa (Hukuncin cikin Alkur'ani ya shafe hukuncin littatafan baya). sai ka yi hukunci a tsakãninsu da abinda Allah Ya saukar kuma kada ka bĩbiyi son zũciyõyinsu daga abinda ya zo maka daga gaskiya. Ga kõwanne daga gare ku Mun sanya sharĩa da hanya (ta bin ta). Kuma dã Allah Yã so, dã Yã sanya ku al'umma guda, kuma amma dõmin Ya jarraba ku a cikin abinda Ya bã ku. Sai ku yi tsere ga ayyukan alheri. Zuwa ga Allah makõmarku take gabã ɗaya. Sa'an nan Ya bã ku lãbãri ga abinda kuka kasance kunã sãɓãwa a cikinsa"

"Kuma ka yi hukunci a tsakãninsu da abinda Allah Ya saukar kuma kada ka bĩbiyi son zũciyõyinsu, kuma ka yi saunar su fitine ka daga sãshen abinda Allah Ya saukar zuwa gare ka. To, idan sun juya bãya, to, ka sani cewa, kawai Allah yana nufin Ya sãme su da masĩfa ne sabõda sãshen zunubansu. Kuma lalle ne, mãsu yawa daga mutãne, haƙĩƙa, fãsiƙai ne."

"Shin, hukuncin Jãhiliyya suke nema? Kuma wane ne mafi kyau ga hukunci daga Allah sabõda mutãne waɗanda suke yin yaƙĩni (tabbataccen ĩmãni)?" Surah Al-Maʾidah aya ta 48 zuwa ta 50.

أدع إلى سبيل ربك بالحكمة و الموعظة الحسنة و جادلهم بالتي هي أحسن إن ربك هو أعلم بمن ضل عن سبيله و هو أعلم بالمهتدين

Ka yi kira zuwa ga hanyar Ubangijinka da hikima da wa'azi mai kyau kuma ka yi jãyayya da su da magana wadda take mafi kyau. Lalle ne Ubangijinka Shĩ ne Mafi sani ga wanda ya ɓãce daga hanyarSa, kuma Shi ne Mafi sani ga mãsu shiryuwa. Surah An-Naḥl aya ta 125.

A yanzu Annabi yayi wafati amma waɗanda suka gaje shi wajen isar da sako suna nan, watau Malamai na gari waɗanda ke kan Sunnarsa SAW. Tare da hadin kan Shugabanni da yardar Allah sakon zai isa.

7. YANAYIN AL'UMMAR DUNIYA A YAU DANGANE DA ADDINI.

Duk da aiko waɗannan manyan Manzanni masu Daraja da Albarka, wadanda suka isar da saƙon da Ubangijisu Ya aiko su da shi na Bushara da Gargadi ga al'ummomi lokuta daban-daban, har zuwa na ƙarshensu, shin an koma kan Addini ɗaya ƙwal?

A'a. To saboda me?

Saboda Kyakkyawa da Mummunar Kaddarar Allah ta rigaya ta faɗa kan al'umma mabanbanta Alkibla (masu rabo da taɓaɓɓu). Allah SWT Ya ce:

ولو شاء ربك لجعل الناس أمة واحدة و لا يزالون مختلفين

إلا من رحم ربك و لذالك خلقهم و تمت كلمة ربك لأملأن جهنم من الجنة و الناس أجمعين

"Kuma dã Ubangijinka Ya so, dã Yã sanya mutãne al'umma guda. Kuma bã zã su gushe ba sunã mãsu sãɓãwa jũna."

"Sai wanda Ubangijinka Ya yiwa rahama, kuma dõmin wannan ne Ya halicce su. Kuma kalmar "Ubangijinka" Lalle ne zã Ni cika Jahannama da aljannu da mutãne gaba ɗaya ta cika". Surah Hud aya ta 118 da 119.

و لقد ذرأنا لجهنم كثيرا من الجن و الإنس لهم قلوب لا يفقهون بها و لهم أعين لا يبصرون بها و لهم ءاذان لا يسمعون بها أولاءك كالأنعام بل هم أضل أولاءك هم الغافلون

"Kuma lalle ne, haƙĩƙa, Mun halitta sabõda Jahannama, mãsu yawa daga aljannu da mutãne, sunã da zukãta, ba su fahimta da su, kuma sunã da idãnu, bã su gani da su, kuma sunã da kunnuwa, ba su ji da su; waɗancan kamar dabbobin gida suke. Ã'a, sũ ne mafi ɓacẽwa (wauta, rashin kan gado da hankali); Waɗancan sũ ne gafalallu." Surah Al-Aʿraf aya ta 179.

Duk da haka wajibi ne kiran Al'umma komawa kan Wannan Tafarkin Miƙaƙƙe, saboda wani sai Allah Ya nufe shi da jin kiran ne, sannan yake faɗakuwa tare da samun taufiƙin Allah, sannan ya shiryu ya koma kan tafarki Madaidaici (Musulunci). Duk wannan yana cikin Kaddarar Allah kan bayinSa. Allah SWT Ya ce:

و ذكر فإن الذكرى تنفع المؤمنين

Kuma ka tunãtar, dõmin tunãtarwa tanã amfãnin mũminai (Wanda yake mumini ne a yanzu, da kuma wanda cikin Ilimin Allah Ya san zai zama mumini nan gaba kaɗan). Surah Adh-Dhariyat aya ta 55.

Musulmai nawa ne suka gyaru da jin wa'azi suka daina Bidi'a da Shirka da ragowar nau'ikan sabo? Maguzawa nawa ne suka karɓi Musulunci da jin Tunatarwa? Yahudawa da Kiristoci nawa ne suka shigo Musulunci da jin saƙon da ke cikin Littafin Karshe, Alƙur'ani (Final Testament)? Allah Ya faɗi Gaskiya.

Sannan Hadithi daga Manzon Allah SAW yana cewa:

أخبرنا قتيبة بن سعيد قال حدثنا يعقوب عن ألي حازم قال أخبرنا سهل بن سعد أن رسول الله صلى الله عليه و سلم قال يوم خيبر لأعطين هذه الرعاية غدا رجلا يفتح الله على يديه يحب الله و رسوله و يحبه الله و رسوله فلم أصبح الناس غدوا على رسول الله صلى الله عليه و سلم كلهم يرجو أن يعطاها قال أين علي بن ألي طالب فقالوا هو يا رسول الله يشكدتكي عينيه قال فأرسلوا إليه فأتي به فبصق في عينيه و دعا له فبرأ حتى كأن لم يكن به وجع فأعطاه الرعاية فقال علي يا رسول الله أقاتلهم حتى يكونوا مثلنا قال أنفذ على رسلك حتى تنزل بساحتهم ثم أدعهم إلى الإسلام فوالله لأن يهدي الله بك رجلا خير لك من أن يكون لك حمرِ النعم

8093 "............ Allah Ya shiryar da mutum ɗaya ta hannunka yafi alkhairi a gare ka, akan ka sami jajayen raƙuma (sune mafi darajar dukiya a lokacin). An-Nasa'i Sunanul kubrah Hadith na 8093.

Duba Bukhari Kitabuj jihad H2942 p125 v4

8) KOKARIN KAFIRAI DA MULHIDAI WAJEN RUSA ADDININ GASKIYA A JIYA DA YAU.

Allahu Akbar - Allah Mafi Girma, Subhanallahi - Tsaki ya tabbata ga Allah. Allah Mahaliccin da, kuma Masanin da, Allah Mahaliccin yanzu, kuma Masanin yanzu, Allah Mahaliccin gobe kafin ta zo, kuma Masanin gobe kafin ta zo, Yake faɗa mana cikin LittafinSa Mai Girma tun fiye da shekaru dubu ɗaya da ɗari huɗu (1400) da suka gabata:

8.1 HUJJA DAGA CIKIN ALKUR'ANI

يريدون ليطفعوا نور الله بأفواههم و الله متم نوره ولو كره الكافرون

"Sunã nufin su bice hasken Allah da bãkunansu alhãli kuwa Allah Mai kammala hasken Sa ne, kuma kõ da kãfirai sun ƙi." Surah Aṣ-Ṣaff aya ta 8.

و لن ترضى عنك اليهود و لا النصارى حتى تتبع ملتهم قل إن هدى الله هو الهدى و لإن اتبعت أهوا ءهم بعد الذي جاءك من العلم ما لك من الله من ولي و لا نصير

Kuma Yahũdu bã zã su yarda da kõme daga gare ka ba, kuma Nasãra bã zã su yarda ba, sai kã bi irin aƙidarsu. Ka ce: "Lalle ne, shiriyar Allah ita ce shiriya." Kuma lalle ne idan ka bi son zũciyõyinsu a bãyan abinda ya zo maka na ilmi, bãka da, daga Allah, wani majiɓinci, kuma bãbu wani mataimaki." Surah Al-Baqarah aya ta 120.

و قالوا كونوا هودا أو نصارى تهتدوا قل بل ملت إبراهيم حنيفا و ما كان من المشركين

"Kuma suka ce: "Ku kasance Yahũdãwa ko Nasãra, kwã shiryu. "Ka ce: "A'a aƙidar Ibrãhĩm dai, maikarkata, zuwa ga gaskiya, kuma bai kasance daga mãsu shirki ba." Surah Al-Baqarah aya ta 135.

Kenan aƙidar Yahudu da Nasara a yau ba ta kan Gaskiya, kuma mai karkata ce ga Shirka, saɓanin Aƙidar Annabi Ibrahim mai cike da Gaskiya da Tauhidi. Dubi cikin waɗancan Addinan a yau, zaka fahimci tabbas abin haka yake a zahiri a yau.

يسألونك عن الشهر الحرام قتال فيه قل قتال فيه كبير و صد عن سبيل الله و كفر به و المسجد الحرام و إخراج أهله منه أكبر عند الله و الفتنة أكبر من القتل و لا يزالون يقاتلونكم حتى يردوكم عن دينكم إن استطاعوا و من يرتدد منكم عن دينه فيمت و هو كافر فألاءك حبطت أعمالهم في الدنيا و الآخرة و أولاءك أصحاب النار هم فيها خالدون

Suna tambayar ka game da Watan Alfarma: yin yãƙi a cikinsa. Ka ce: "Yin yãƙi a cikinsa babban zunubi ne, kuma hani daga hanyar Allah, da kuma kãfirci da Shi, da kuma Masallaci Tsararre, da Kuma fitar da mutãnensa daga gare shi, shi ne mafi girman zunubi a wurin Allah."

Kuma fitina ita ce mafi girma daga kisa. Kuma bã su gushẽwa suna yãƙinku har su mayar da ku daga barin addininku idan za su iya. Kuma wanda ya yi ridda daga gare ku ga barin addininsa har ya mutu alhãli kuwa yana kãfiri, to, waɗannan ayyukansu sun ɓãci a cikin dũniya da Lãhira. Kuma waɗannan abõkan Wuta ne, sũ a cikinta madauwama ne. Surah Al-Baqarah aya ta 217.

ودت طاءفة من أهل الكتاب لو يضلونكم و ما يضلون إلا أنفسهم و ما يشعرون

Wata ƙungiya daga Mutãnen Littãfi sun yi gũrin su ɓatar da ku, to, ba su ɓatar da kõwa fãce kansu, kuma bã su sansancewa!" Surah Ali-ʿImran aya ta 69.

إن الذين كفروا ينفقون أموالهم ليصدوا عن سبيل الله فسينفقونها ثم تكون عليهم حسرة ثم يغلبون و الذين كفروا إلى جهنم يحشرون

Lalle ne waɗanda suka kãfirta, sunã ciyar da dũkiyõyinsu, dõmin su kange daga hanyar Allah; to, zã su ciyar da ita, sa'an nan kuma ta kasance nadãma a kansu, sa'an nan kuma a rinjãye su. Kuma waɗanda suka kãfirta zuwa ga Jahannama ake tãra su;" Surah Al-Anfal aya ta 36.

إن شر الدواب عند الله الذين كفروا فهم لا يؤمنون

Lalle mafi sharrin dabbõbi a wurin Allah, sũ ne waɗanda suka kãfirta, sa'an nan bã zã su yi ĩmãni ba." Surah Al-Anfal aya ta 55.

Su waɗannan kafirai da mulhidai, tun can baya, wasunsu sunyi ta shiga Musulunci domin gurɓata shi. Wasu kuma Musulmi ne waɗanda suka zame. A rubuce yake cikin Tarihi, cewar mutane irin su Ibn Arabi wanda asalinsa Sunni ne amma ya zame ya zama ɗan falsafa kuma mutum na farko da ya ƙirƙiro sufanci (tasauwuf) 560-635AH, ya jingina shi ga Addinin Musulunci. Wadda da shine (sufanci) aka JIRKITA haƙiƙanin

koyarwar fiyayyen halitta Annabi SAW ta Tauhidi (kaɗaita Allah cikin bauta da neman agajin gaggawa gare Shi, Shi kaɗai watau Allah) da kuma KIN bin Sunnah (koyarwar Annabi SAW shi kaɗai cikin duk wani sha'ani na Addinin Musulunci, zamantakewa da mu'amala).

Sun mayar da mutane mushrikai masu da'awar kowa da komai Allah ne. Wasunsu kuma sun kasa banbance tsakanin Mahalicci (Allah SWT) da abinda Allah Ya halitta na bayinSa kamar Annabawa da Salihan bayi, ta yadda suke bauta musu. Irin waɗannan mutanen suna da'awar komai ka gani tattare dasu a yau to Annabi ne ko Shehi ya basu. Ko ina suka ajiye Allah oho? Sannan in sun shiga musifar ba zata (bagatatan), Shehi ko Annabi suke kiran agajinsa domin ya kuɓutar da su. Kenan sun ɗauki hakkin Allah sun baiwa Annabi ko Shehi. Kai akwai masu ganin ma idan ka kai wani matsayi ba sai kayi Sallah ba. Annabi da Sahabbansa da Tabi'ai da waɗanda suke biye da su da duk wani Musulmi na gari yakan rasu ne, yana mai yin Sallah koda yaushe (akan lokacin ta kuma cikin jam'i). Saboda Manzon Allah SAW ya ce: "Banbancin mu da su (watau kafirai) Sallah". Da wannan Nassin duk wanda ya bar Sallah ya kafurta.

Irin wannan Addinin na yan Tijjaniyya da Kadiriyya da Shi'a, Wallahi, Tallahi, Billahi Annabi bai san shi ba, haka Sahabbansa da Tabi'ai da waɗanda suka biyo bayansu.

Wannan kuma ita ce babbar fitina da musifa cikin al'ummar Musulumai a yau musamman a ƙasar Hausa. Ta yadda da yawa suna Sallah amma kuma mushrikai ne. Sannan sun zare takwabi domin yaƙar masu kiransu da su komo kan Tauhidin kaɗaita Allah da bauta Shi kaɗai, da kuma kaɗaita Manzon Allah shi kaɗai da biyayya domin koyon Addinin da za a bautawa Allah da shi. Bayan wannan suna watsa farfaganda da cewar waɗancan masu Tauhidin, sune maƙiya Allah da ManzonSa

wadda jahilan mabiyansu suka yarda da su kan wannan ƙazaf da makirci. Har takai ana zargin wasunsu da makirci tare da kashe manyan malaman waccan Madaidaiciyar tafiya ta Manzon Allah SAW cikin ƙasa da shekaru ashirin. Ba za mu manta da kisan gillar da akaiwa Ɗan meshiya Sakkwato, da Sheikh Ja'afar Mahmoud Adam Kano, da Sheikh Auwal Albanin Zariya, yanzu kuma Sheikh Idris Abdul'aziz Bauchi (koda yake wannan na ƙarshen an ce ya rasu sakamakon rashin lafiya a kan gadonsa). Allah Ya yi musu rahama kuma Ya karɓe su duka Shahidai. Sannan su kuma mulhidai makirai kada su mutu su zauna su yi jiran duniya.

Wannan kenan.

A yau ƙungiyoyin cikin gida da na waje, da ƙasashen yamma sun kai matuƙa wajen ganin sun raba Musulmi da Addininsa kamar yadda su suka yi baran-baran da nasu Addinin. Shirye-shiryensu na Sharri cikin kafafen sadarwa na zamani domin rusa tarbiyyar Musulmi gaba ɗayanta, suna ta watsoshi. Haka makircinsu na ƙirƙiro ƙungiyoyi cikin Addinin Musulunci tare da rubutawa waɗannan ƙungiyoyin gurɓatattun littattafai domin gurɓata aƙidar Musulmi ta Tauhidi a bayyane yake. Har kullum nakan so buga misali da maganganun Asheikh Dakta Farfesa Dawud Ujobi dangane da Jawahiril Ma'ani, kundin yan Tijjaniyya. Haka Turawan Yamma da ƙarfin tuwo suka tilasta mana barin aiki da Hukunce-Hukuncen dake cikin Alƙur'ani sai ɗan abinda ba a rasa ba, ta hanyar tilasta mana bin tsari na "Secularism" a cikin ƙasar da mafi yawan Al'ummatta Musulmai ne. Bahaushe yace "kifi na ganinka mai jar koma".

8.1.1 JAN HANKALI GA MUMINAI KADA SU YARDA SU YIWA KAFIRAI ƊA'A CIKIN BIN SON ZUCIYAR KAFIRAN.

يآ أيها الذين ءامنوا إن تطيعوا فريقا من الذين أوتوا الكتاب يردوكم بعد إيمانكم كافرين

"Ya ku waɗanda suka yi ĩmãni! Idan kun yi ɗã'a ga wani ɓangare daga waɗanda aka bai wa Littãfi, zã su mayar da ku kãfirai a bãyan ĩmãninku!" Surah Ali-ʿImran aya ta 100.

و إن تطع أكثر من في الأرض يضلوك عن سبيل الله إن يتبعون إلا الظن و إن هم إلا يخرصون

إن ربك هو أعلم من يضل عن سبيله و هو أعلم بالمهتدين

"Kuma idan ka bi mafiya yawan waɗanda suke a cikin ƙasa da ɗã'a sunã ɓatar da kai daga hanyar Allah. Ba su bin kõme sai ƙaddari-faɗi (molon ka) suke yi."

"Lalle ne Ubangijinka Shĩ ne Mafi sani ga wanda yake ɓacẽwa daga hanyarsa kuma Shi ne mafi sani ga masu shiryuwa." Surah Al-An'am aya ta 116 da 117.

لتبلون في أموالكم و أنفسكم و لتسمعن من الذين أوتوا الكتاب من قبلكم و من الذين أشركوا أذى كثيرا و إن تصبروا و تتقوا فإن ذالك من عزم الأمور

"Lalle ne zã a jarraba ku a cikin dũkiyarku da rãyukanku, kuma lalle ne kuna jin cũtarwa mai yawa daga waɗanda aka bai wa Littãfi a gabãninku da kuma waɗanda suka yi shirki. Kuma idan kun yi haƙuri, kuma kuka yi taƙawa, to lalle ne, wannan yana daga manyan al'amurra." Surah Ali-ʿImran aya ta 186.

لا يغرنك تقلب الذين كفروا في البلاد

متاع قليل ثم مأواهم خهنم و بأس المهاد

"Kada jujjuyawar waɗanda suka kãfirta a cikin garũruwa ta rũɗe ka."

"Jin dãɗi ne kaɗan sa'an nan makõmarsu Jahannama ce, kuma tir da shimfiɗa ita!" Surah Ali-ʿImran aya ta 196 da 197.

8.1.2. NARKON AZABA DA WULAKANCI KAN MUSULMAN DA SUKA YIWA ALKUR'ANI KUNNEN UWAR-SHEGU, A DUNIYA DA LAHIRA.

و من أعرض عن ذكري فإن له معيشة ضنكا و نحشره يوم القيامة أعمى

قال ربي لم حشرتنى أعمى و قد كنت بصير

قال كذلك أتتك ءاياتنا فنسيتها و كذلك اليوم تنسى

وكذا لك نجزى من أسرف ولم يؤمن بأيات ربه ولعذاب الآخرة أشد و أبقى

"Kuma wanda ya bijire daga ambatõ Na (Alƙur'ãni Na), (ya abka cikin saɓo da Shirka) to, lalle ne rãyuwa mai ƙunci ta tabbata a gare shi, kuma Munã tãyar da shi a Rãnar ƙiyãma yanã makãho."

Ya ce: "Ya Ubangiji! Don me Ka tãyar da ni makãho alhãli kuwa nã kasance mai gani?"

Ya ce: "Kamar wancan ne ãyõyin Mu suka jẽ maka sai ka mance su, kuma kamar haka ne a yau ake mance ka."

"Kuma kamar haka Muke sãkawa wanda ya keta haddi (ya ƙetare iyaka), kuma bai yi ĩmãni da ãyõyin Ubangijinsa ba. Kuma lalle ne azãbar Lãhira ce mafi tsanani, kuma mafi wanzuwa". Surah Ṭā-Hā aya ta 124 zuwa 127.

A Ranar Kiyama lallai masu taurin kai sun shiga uku:

فذوقوا بما نسيتم لقاء يومكم هذا إنا نسيناكم وذوقوا عذاب الخلد بما كنتم تعملون

"To, ku ɗanɗana sabõda abin da kuka manta na haɗuwa da ranarku wannan. Lalle Mũmã Mun manta da ku, kuma ku dãnɗani azãbar dawwama sabõda abin da kuka kasance kunã aikatãwa." Surah As-Sajdah aya ta 14.

9) KAMMALAWA

Idan muka yi la'akari da duk abinda ya gabata na Ayoyin Alƙur'ani da Hadithan Manzon Allah SAW, zamu fahimta tare da yarda cewar Al'ummar Duniya, a yau ko gobe, ba za ta taɓa komawa kan Addini ɗaya ƙwal ba ko wanne irine, watau daga na Gaskiyar har na Karyar. Domin ƙaddarar Allah ta riga ta gabata a kanta (Al'ummar). Wannan zai daɗa tabbatuwa a gareka da faɗînSa Subhanawu Wa Ta'ala:

و ما أكثر الناس ولو حرصت بمؤمنين

Kuma mafi yawan mutãne ba zasu zama mãsu ĩmãni ba, kõda kãyi kwaɗayin haka." Surah Yusuf aya ta 103.

قل لا يستوى الخبيث و الطيب و لو أعجبك كثرة الخبيث فاتقوا الله يآولي الألباب لعلكم تفلحون

"Ka ce: "Mummuna da mai kyau bã su daidaita, kuma kõ dã yawan mummunan yã bãka sha'awa. Sabõda haka kubi Allah da taƙawa, yã ma'abuta hankula ko la'alla zã kuci nasara." Surah Al-Maʾidah aya ta 100.

Haka abin yake cikin Hadithin Manzon Allah SAW inda aka rubuto cewar:

حدثنا أحمد بن حمبل و محمد بن يحي بن فارس قالا : حدثنا أبو المغيرة حدثنا صفوان و حدثنا عمرو بن عثمان حدثنا بقية حدثني صفوان نحوه قال: حدثني أزهر بن عبد الله الحرازي عن أبي عامر الهوزني عن معاوية بن أبي سفيان أنه قام فينا فقال:ألا إن رسول الله صلى الله عليه و سلم قام فينا فقال:ألا إن من قبلكم من أهل الكتاب افترقوا ثنتين و سبعين ملة و إن هذه الملة ستفترق على ثلاث و سبعين ملة:ثنتان و سبعون في النار و واحدة في الجنة و هي الجماعة ـراد ابن يحيى و عمرو في

حديثهما:و إنه سيخرج في أمتي أقوام تجارى بهم تلك الأهواء كما يتجارى الكلب لصاحبه و قال عمرو :الكلب لصاحبه لا يبقى منه عزق و لا مفصل إلا دخله

4597. Hadithi daga baban Amir al Auzani cewar Mu'awiyya ɗan Abu Sufyan ya tsaya cikinmu yace "Manzon Allah (SAW) ya tsaya cikinmu yace "mutanen da suka gabaceku mazowa littafi (Yahudu da 'Yan Mishan Kiristoci) sun karkasu kashi saba'in da biyu, kuma wannan al'umma (Musulmai) zasu karkasu saba'in da uku, waɗanda saba'in da biyu daga cikinsu duk Wutã zasu shiga, kaso ɗaya ne 'Yan Aljanna. Sune waɗanda basu rarraba ba, suke tare da Jama'a. Ibn Yahya da Amr sun ƙara cikin hadithinsu cewar "waɗansu mutane zasu bayyana cikin wannan al'ummar tawa, son zuciya da son Jin daɗin duniya zai lulluɓesu kamar cutar mahaukacin kare wadda bata barin wata jijiya ko ƙashi na maras lafiya face sai ta shigeta"'". Sahih daga sunan Abu Dawud, Kitabus Sunnah

Manzon Allah SAW ba ya ƙarya, kenan tabbas abin haka yake. Kuma a zahiri yake a yau ba gobe ba. Haƙiƙa a cikin Musulmai an rarrabu, rarrabuwar da takai wasu sun koma yin Shirka tsundum saboda son zuciya da son Jin daɗin Duniya kamar yadda aka yi tsokaci cikin wannan Hadithi. Allah Ya sauwaƙe. Wannan kenan cikin Addini ɗaya an rarraba an kauce hanya, kaucewar da zata kai mutum Wutar Jahannama, ina kuma ga ragowar addinai saɓanin Musulunci?

Waɗannan Ayoyin Alƙur'ani da Hadithan Manzon Allah SAW suna tsokaci kan cewa lallai kowanne lokaci a doron ƙasar nan, sai an sami masu biyayya ga Addinin Allah da kuma kangararru maƙiya Addinin Allah. Saboda haka, me yasa zaka damu kanka, har ka sami ƙuncin zuciya akan mushrikai da 'yan bidi'a da yan duba da bokaye da ragowar da kafurai?

Idan Allah Ya ƙaddara maka kasancewa cikin na gari masu bin Allah cikin Addinin da Allah Ya Shar'anta a bi a lokacinka, sai kayi ta godewa

Allah tare da Addu'ar dauwama akai, ba tare da ka zame ba har mutuwarka. Domin zaɓi ne daga Allah SWT ba dabarar ka ce ko ƙarfin ka ba.

Ragowar kuma waɗanda ba irinka ba, tausaya musu za kayi tare da yi musu Addu'ar SHIRIYA. Ba gaba da ƙiyayya za kayi dasu ba ta fitar hankali wadda ta sãɓãwa Shariya. Ko kuma kayi abinda zai halakar da kanka saboda su.

أفمن زين له سوء عمله فرءاه حسنا فإن الله يضل من يشاء و يهدي من يشاء فلا تذهب نفسك عليهم حسرات إن الله عليم بما يصنعون

Shin to, wanda aka ƙawãta masa aikinsa, har ya gan shi mai kyau (yanã daidai da waninsa)? Sabõda haka, lalle, Allah Yanã ɓatar da wanda Yake so, kuma Yanã shiryar da wanda Yake so, sabõda haka kada ranka ya halaka a kansu dômin baƙin ciki. Lalle Allah Masani ne ga abinda suke sanã'antawa. Surah Faɗir aya ta 8.

Ba kuma amincewa za kayi da su ba cikin duk son zuciyar da suka zo da shi wanda ya sãɓãwa abinda kake kai. Babu raba ƙafa ko haɗa baki ko sassautawa "No compromise" abinda Bature yake cewa cikin Addinin ka.

Allah SWT Ya umarce mu da yin Musulunci gaba ɗayansa ba rabi da rabi kamar yadda Kiristoci da Yahudawa suke yi ba. Duk Dokokin dake cikin Littattafansu kawai karantawa sukeyi su wuce amma ba sa ɗabbaƙasu a zarihi. Kai kace wasu Tatsuniyoyi suke karantawa. Allah Ya sauwaƙe.

Gurin da Allah SWT Ya baka dama ka zare takwabi akan wanda ba irinka ba, shine lokacin da ya hana ka yin Addininka ko kuma ya hanaka ɗabbaƙa Dokokin Addinka kamar yadda Allah SWT Ya umarceka. Anan

kam babu ja da baya, imma NASARA imma SHAHADA. Amma matuƙar bai hanaka yin Addininka ba kamar yadda yake a Asali, to Allah SWT Ya ce ka ce da kafirai:

قل يا أيها الكافرون

لا أعبد ما تعبدون

و لا أنتم عابدون ما أعبد

و لا أن عابد ما عبدتم

و لا أنتم عابدون ما أعبد

لكم دينكم و لي دين

Ka ce: "Ya kũ kãfirai!"

"Bã zan bautãwa abinda kuke bautãwa ba."

"Kuma kũ, ba ku zama masu bautawa abinda nake bautãwa ba."

"Kuma nĩ ban zama mai bautãwa abinda kuke bautãwa ba."

Kuma kũ, ba ku zama mãsu bautãwa abinda nake bautãwa ba."

"Addininku na garẽ ku, kuma addinina yanã gare ni." Surah Al-Kafirun aya ta 1 zuwa ta 6.

A karshe Allah SWT Yana daɗa jan hankalinmu mu Musulmai da cewa:

أفحكم الجاهلية يبغون و من أحسن من الله حكما لقوم يوقنون

Shin, hukuncin Jãhiliyya suke nema? Kuma wane ne mafi kyau ga hukunci daga Allah sabõda mutãne waɗanda suke yin yaƙĩni (tabbataccen ĩmãni)? Surah Al-Maʾidah aya ta 50

و ما الحياة الدنيا إلا لعب و لهو و للدار الآخرة خير للذين يتقون أفلا تعقلون

Kuma rãyuwar dũniya ba ta zama ba, fãce wãsa da shagala, kuma lalle ne, Lãhira ce mafi alhẽri ga waɗanda suka yi taƙawa. Shin, ba za ku yi hankali ba? Surah Al-Anʿam aya ta 32

Ya ɗan uwa cikin neman alkhairi da falalar Allah SWT domin kyautata rayuwarka da samun damar bautawa Ubangijinka cikin natsuwa da walwala, albishirinka! Allah AWJ Ya ce:

من عمل صالحا من ذكر أو أنثى و هو مؤمن فلنحيينه حيواة طيبة و لنجزينهم أجرهم بأحسن ما كانوا يعملون

Wanda ya aikata aiki na ƙwarai daga namiji kõ kuwa mace, alhãli yanã mũmini, to, haƙĩƙa Munã rãyar da shi, rãyuwa mai dãɗi. Kuma haƙĩƙa Munã sãkã musu lãdarsu da mafi kyãwun abinda suka kasance sunã aikatãwa. Surah An-Naḥl aya ta 97.
Babban Aiki na ƙwarai yakan fara ne daga Zuciya cikin ƙudure aƙidar Tauhidi, na Gaɓɓai kuma shine Sallah (akan lokacinta kuma cikin jam'i ga namiji), Azumi (watan Ramadan), Zakka, Hajji ga mai iko. Sauran kuwa sun haɗa da Ɗabi'a mai kyau, bin Sunnar Manzo, Ciyarwa ga mabuƙata, biyayya ga Mahaifa, karanta Alƙur'ani, fahimtar ma'anoninsa, aiki da shi, tadabburi cikinsa, karantar dashi, da sauransu. Sai kuma barrantuwa daga Shirka komai ƙanƙantarta da manyan Saɓo.
Kuma SHARAƊIN karɓar Aikin ƙwarai shine mutum ya kasance mumini (Musulmi wanda ba ya shirka da wadda ba ta shirka). Da wanda ba Musulmi ba (kafiri) zai ciyar da duk abinda ke cikin Duniya domin kyautatawa Al'umma, ba za a karɓa masa ba, kenan bashi da ladan komai a gurin Allah Ranar Gobe Kiyama, domin ba Mumini ne ba.
Rayuwa mai daɗi ita ce Allah Ya hore maka nemanka da samunka da tasarrufinka cikin samunka (komai girmansa ko ƙanƙantarsa), cewa duk su kasance cikin Halal (abinda Allah Ya ke so), ba cikin Haram (abinda Allah Ya ke ƙi) ba, a nan Duniya. Ranar Gobe Kiyama kuma Allah Ya

saka ka cikin AljannarSa kuma Ya kare ka daga shiga Wutar Jahannama. Alhamdu lilLahi.

A taƙaice yana da kyau ɗan uwa ya duba Tafsirin Qurdabi da Ibn Kathir da Ibn Jarir At-Ɗabari da sauran Tafasir domin ƙara fahimtar ma'ananonin ayoyin da aka kawo cikin wannan littafi. Da fatan Allah Ya amfane mu da shi.

Ya Allah muna roƙonKa, muna tawassuli da waɗannan Ibadu da muke yi cikin wannan Wata mai girma Watan Ramadan Watan Alƙur'ani, da Ka ƙarfafemu ɗabbaƙa DokokinKa ko ina a Nijeriya. Musulmi ya bi Dokokinsa na Musulunci, waninsa kuma yabi dokokin da yaga sun dace da shi "period".

Alhamdu lillah, wassalatu wassalamu 'ala malla nabiyya ba'adah.

Mawallafi: Bldr. Ibrahim Muhammad Ɗanƙyauri 08022333154 / 08034549647

Tammat Ramadan 1446 // Maris 2025. Gyara kurakuran bugu da sabuntawa Shauwal 1446 // Abrilu 2025.